ZURFIN CIKI book 1 part 1
Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 02:16
UUmmi tana tafe tana yan wakokinta, tareda gudu hade da tsalle. cinikin ummi ne gudu, sam bata tafiya a hankali.daga can gefe ta hango wata yarinya wadda bazata wuce sa'arta ba. tace,"yauwa,ga firdausin data tsokane ni" ta nufi wurinta ,tasha gabanta ta rike kugu. "fiddausi wa kike tsokana? fiddausi tace "ban tsokane ki ba fa".cikin tsoro tayi maganar .ummi ta shako mata wuya. ina jin lokacin da kika ce ummi tsiga.ban ce ba inji fiddausi .ummi ta hankada ta tare da cewa "Allah yaso ki." nikan garin da fiddausin tayi ya tarwatse a kasa tace "kin gani ko? wallahi sai kin biyani"ta soma kuka,ummi ta sheka da gudu,sai gida. tana ajiye man gyadan data siyo ta nufi ba daki don fitsari ya matse ta .umma dake zaune tana fadin. "da mutum!da mutum!!" saida ummi ta bude . Ganin yaya Abba tayi,da gudu ta juyo ta fada dakin umma,jiki na bari bayan tayi bol da dakakken yajin da umma ta daka zata soya mai don cin abincin rana. sai kuma ta tuna cewa bata tsira ba,don Abba tsaf zai binciko ta.ta fito da gudu ta nufi dakin tsohuwa. tsohuwar tana sallar azahar.ummi ta tsallake ta ta kutsa kasan gado.nan ma tayi ciki da furar da tsohuwar keson sha da zarar ta idar da sallah. Alhaji babba tasa ya aiko mata da furar daga kasuwa.don tasha da rana. Abba ya fito wanka ranshi a bace.dakin umma ya nufa yana fadin "ummi ke ummi zonan" Ya samu Umma tana tattara yajin da Ummi ta zubar, tana fada. Ya ce, "Umma ban san irin dukan da zan wa Ummi ba yau. Ta ce,"Abba ka mata dukan mutuwa, na gaji da halin Ummi. Yarinya sai ka ce 'yar fata? Ka dubata ta tafi dakin Tsohuwa, don ta san zata hana a dake ta." Ya ce,"Allah sai dai Tsohuwa ta yi ta fadanta, amma ba zan barta ba. Ya juya zai tafi, suka ji muryar Tsohuwa tana fadin. Ba zan yi fada ba, ka kashe ta ka ji mai sunan Malam, ba na son ka barta da rai. Ta dubi Umma" ke kuma Suwaiba

dama kin san ba za ki daraja sunana ba ki ka sa a ka sa miki don kiji dadin ci min fuska?" Umma ta ce," Ba haka ba ne Tsohuwa, Ummi ba ta yo halinki ba. Ita fa rashin hankali ne da ita. Yayanta fa ke wanka ta zo ta leka shi, nan kuma tazo ta zubar min da barkono. Abba ya ce, "Umma don Allah kiyi shiru ki kyale Tsohuwar nan, ai ita ta 6ata Ummin, duk abn da yarinyar nan tayi sai ta hana a yi mata fada. Uhm duk fadanki yau sai na dake ta, ba sunan ki ba in ma kece,"Tsohuwa tasa kuka gami da salati. "Yanzu mai sunan Malam ni ka ke fadawa haka?" ya ce, "An fada miki." Umma ta ce, "kai Abba zan sa6a maka jeka." Ta juyo wurin Tsohuwa, Don Allah kiyi hakuri............... Maman Fiddausi ce tayi sallama tare da Fiddausin suka shigo. Ran Maman Fiddausin a 6ace, ta tsaya rike da gari a hannunta ta dubi Umma. Ta ce, Umman Abba dubi abn da Umminki tayi min don Allah, yarinyar nan tayo nika da kyar," tun safe sai yanzu na samu, amma ta zubar min." Abba ya ce, Kinga halinta ko?" Tsohuwa ta ce, "Wannan ba matar Bala ba ce?" Maman Fiddausi ta ce, "Ni ce." Ta ce," To kije kije ki nemi wanda ya zubar da garinki, Ummi ko fita ba tayi ba. Umma ta ce, " Ta fita Tsohuwa, na aike ta siyan mai." Tsohuwa ta ce," Tsokanarta a ka yi to. Umma ta amshe abin garin ta zuba musu, sannan ta ce, "Don Allah Tine kiyi hkr." Abba ya nufi daki. Sai da ya shirya tsaf, sannan ya dauki belt ya nufi cikin gida, dakin Tsohuwa ya shiga kai-tsaye kasan gado ya nufa. Ya jawo ta, ta soma kurma ihu. Daya ya lafta mata amma ta dane shi tare da cukwikuye belt din tana ihu. Tsohuwa ta iso tana dukanshi a baya, fadi take "Za ka kasheta ne? Jama"a kuyo dauki. Haushin hakan yasa shi damko kanta ya shiga zuba mata kola, ya sirmiyota ya shiga lafta da takalminshi, tunda ta hana belt din. Sai da ya mata tas, sannan ya fita ya bar su, Tsohuwa na kuka Ummi na kuka. , Sai da komai ya natsa ta leka ta jawo furarta don tasha, sai ta ganta a zube. Ta ce, A" a ke ki ka zubar min da fura?" Ummi ta ce, To ba shi ne

janyo ni ba Yaa Abban. Tsohuwa ta ce, "Ai ko sai ya siyo min furata. Ta mike ta wuce Umma tana rabon abinci, ta nufi soro in da dakin Abba yake (Zaure) Ya fito yana rufe kofa, ta ce "Au za ka fita ba? To ka sawo min furata da ka zubar. Ko kallonta bai yi ba ya rufe kofarshi ya wuce. Ta ce mishi "Aikin bana, in ba siyo min ba ubanka ai ya dawo ko min dare ya sito min. Abba ya ce, Ku ku ka sani. Ra ce, kaima ka sani, dan jakar uba. Ta dawo ciki tana mitar ya cika bakin rai. Umma ta ce, "Ina Abban? Tsohuwa ta ce, "Ya tafi, in bai sai min furata ba ranshi zai 6aci yau a gidannan. Umma ta ce "Ni bai ma ci abinci ba ya fita, ke Ummi zo ki kira min shi, yunwa fa yake ji. Tsohuwa ta ce, "Ba za ta kira shi ba, ya dake ta sannan ta kira shi? Tunda bai barta taci da dadin rai ba, shi ma ba ya ci ba.,, Umma tayi shiry,sai haushin Ummi da take ji kamar ta shake ta ta mutu. Ummi tayi wanka ta zura kayan Mkrnt, tana saka sandal Umma ta ce, "Ina Ummi? Zo nan." Ummi ta tafi tana cewa a ranta. "ALLAH YASA DAKIN YAYA ABBA ZA TA AIKE NI, SAI NA RAMA DUKAN DA YA YI MIN JIYA, DON YANZUN DUK ME YA MIN SAI NA RAMA.........." Umma ta katse mata tunani da cewa,"dauki shayin Abba ki kai masa kada yayi latti,kai shayin ki dawo ki dauki dankalin,yau shi kadai ma nayiwa dankalin." Tace,"nifa?"umma tace "ke kina cin dumame Abba ko ba ya ci,dan haka dan wanda ya rage shi nayi wa." Ummi ta figi kayan tea din ta nufi dakin Abba tana tura baki.tare da sallama bata jira amsa ba,ta daga labule ta fada. Dabi'ar da yake mata fada akai kullum,ya gama saka singiletinshi kenan yana kokarin saka riga. Yace, "wai ke wace irin majanuniya ce?ban ce miki in kinyi sallama sallama sai na amsa za ki shigo ba? sai kawai ta saki tiren,ruwan zafin ya zube masa a kafa,dankalin ya watse kan rigar da zai saka. tayo waje da gudu,sai dakin tsohuwa.ya fito da sauri yana cewa,"umma ta kona ni! ta kona ni!!" da sauri umma ta fito daga dakin Alhaji babba,shima Alhajin na biye da ita yana fadin "wacece ta kona ka?" Yace "ummi ce! ummi

ce!!."nan take Alhaji babba ya rike kafar yana tofa mishi addu'a. Umma ta debo kullun kamu ta zuba mishi,amma duk da haka sai da yan yatsun kafarsa suka kumbura. tsohuwa ta fito daga daki tana fadin,"kai ummi bata ji? wai ni meyasa aka sa mata sunana?" Abba ya kalli tsohuwa cikin takaici yace,"duk ba ke kike daure mata gindi ba?" Umma ta shiga dakin tsohuwa ta janye kayan da tsohuwa ta jera don kada aga ummi,ta janyota tun daga dakin take kwallo da ummi har waje. Alhaji ma yau har dashi aka zane ummi,tsohuwa dai sai yan mitoci take yi,wai yanxu haka ma bata sani bane. Abba dai ranar dai bai je makaranta ba,haka nan da yamma sai da ya saka ummi a dakinshi ya bata gwale-gwale sannan ya zane ta. misalin hudu da rabi na yamma,Ahmad abokin Abba yayi sallama a kofar gidan,Abba ya amsa ya fito. Suna zaune kan dakalin kofar gidan suna hira,sai ga ummi ta yanko da gudu tana waiwayen baya. Ya ce,"zo nan."tazo yace,"kinyo tsokanar fada ko?" tace,"a'a.yace in har tsokana ki kayo zaki sani shegiya mummuna kazama. Ta murguda baki,yasa takalmi ya jefeta,ta shige gida sai ko ga wani yaro jiki duk kwata yayyanshi na biye dashi. ya tambayesu,suka ce "ummi ce ta jefa shi kwata"ya taso yaron har cikin gida ya kamota dakin tsohuwa ya tsareta ta wanke ma yaron jiki,ta kuma wanke kayan. sannan ya zuzzuba mata kola a kai.tsohuwa tana ta yiwa yaran fada,wai ita ma su daina tsokanarta Umma ko lekowa bata yi ba,ya fito ya samu Ahmad yana cewa "kayi hakuri na barka kai kadai." Ahmad yace,"ba komai" sai Abba ya zauna sannan Ahmad ya dube shi. Abba wannan kanwar taka kuwa bata da Aljanu? Abba yace,"ba kowa akanta,sai iskanci." Ahmad yace."a'a,kai dai ku kaita ayi mata rukiyya." Abba yayi dariya,sannan yace kasan Allah ba kowa akan ummi,saboda Alhaji karami ya taba yin wannan tunanin. ya dauke ta yakai ta rukiya bata da komai."Ahmad yace tabdi!,gaskiya in ta isa aure duk wanda ya aureta akwai aiki babba a tare dashi. Abba ya ce,"wane mahaukaci ne ma zaya dibar ma kansa

ummi?"Ahmad ya ce,"sai ai muku hadin ggida..." ya kaima Ahmad naushi a gefen ciki,Ahmad ya kauce yana masa dariya. Abba ya ce,"ka cuce ni,ace in auri ummi ai sai na hada kayana na bar garin nan. nan. Ahmad ya s heke da dariya har da rike ciki.sannan ya ce,"don me? Abba ya ce,"to wannan yarinyar ba sai ta hada maka gobara gida ba?gata kazama ga muni." Ahmad ya ce,"kama dai kuke yi." Abba ya bata rai,"Ahmad bana so.in har da gaske ina kamada ummi ba sai na koma ciki an sake haifana ba. Don Allah ni tashi ma ka tafi,don wallahi da don kai bane kake fada min haka da sai munyi rigima,na tsani ummi,bana sonta sam! Zaune suke a kofar gidan Alhaji babba kan katuwar tabarma,sun jere abinci suna ci. kullum Alhaji babba da Alhaji karami nan suke zama tamkar tagwaye,suna matukar kama. mafi yawancin lokuta ma kaya iri daya suke sakawa,domin Alhaji babba duk kayan daya saya tare yake sai musu. haka nan hula ko takalmi,haka nan matansu baya bambantawa.shima Alhaji karami duk da bai kai samun babba ba yana koyi dashi. Alhaji babba ya kalli karami yace,"Aminu ya zancen makarantar bashir?" Alhaji karami ya dubi wansa ya ce,"Alhaji bashi fa ya fadi jarabawa,jiya na tsare shi da maganar sakamakon jarabawarshi yace bai duba ba,saida yaji nace zan hada shi da Abba suje sannan yace min yaje wai duk ya fadi. Alhaji babba yace,"Ash sha! sai ya maimata shekara kenan?"Alhaji karami ya ce,"to in ma ba zai maimaita ba Alhaji shi ya sani,ba sahura ta bata su ba? shi Abba ai ba haka yayi ba,ka dubi fa yadda yaki aikin kanikancin nan,uwarshi ta zuga shi wai yayi karatu kadai yayi aikin gwamnati. kullum haka sahura take kitsa ma yaran."Alhaji babba yayi yar dariyar takaici,sannan yace"in banda abin sahura yadda kasan nan tamu ta zama waye zaici alwashin aikin gwamnati? ina ce masu digree ne ke yawo ba aiki?" "har masu masters." inji Alhaji karami.ya tashi zaune daga kishingidar da yayi,yace dubi misalin dan abokinnan naka Alhaji buhari." Alhaji babba ya

ce,"kwarai kuwa,mas'ud ba.yanxu ma fa kasuwa yake zuwa,sai yanxun yake koyon kasuwancin." Alhaji karami ya ce,"to daya dora shi a kasuwar fa tun farko?shi yasa na fada ma sahura ta bar yara su hada da sana'ar hannu. Donni dai yaro kamar bashir yanxun ba zan dauki kudina in ba shi ba."Alhaji babba yace,"shi yasa kulum nake kara son Abba,yaron nan da kanshi yace min in kai shi shagon dinki. Har naki suwaiba ta ce,"Alhaji ka kai shi in ya iya sana'ar hannu ko bai samu aikin gwamnati ba zai rike kanshi da sana'ar nan." Alhaji karami ya ce,"to ai kasan ita suwaiba tasan abinda take yi.amma sahura sai addu'a." Sallamar Abba ce ta katse su,ya zauna can gefe sannan ya gaishe su,duk suka amsa tare da tara hankulasu gurinshi. Ya mika ma Alhaji babba kullin takarda tare da cewa "Alhaji gashi maganin (ulser)ne" Alhaji babba ya amsa ya ce,"Abba sarkin amsa magani, a gurin wa ka samo wannan kuma?" ya ce,"Ahmad abokina na raka ya amso ma babanshi,shine nace bari in amso muku" yace to Allah ya saka da alkairi."Alhajikarami yace"dame ake sha?" Abba ya ce,"da madara peak." suka ce"to" daya mike zai shiga gida Alhaji babba yace ya shige da kwanikan abincin. yau kam Abba bacci yake ji da wuri,don haka ya baro shagon dinkinsu wanda ya kan kai goman dare a ciki ya nufo gida. Ya bude dakinshi ya shiga ya cire riga sai singileti da gajeren wando na jeans.ya nufi ciki don ya kama ruwa ya kuma yi wa ummanshi sallama. tsakar gida ya sameta zaune ta zabga tagumi,inda abinda Abba ya tsana shine,yaga ummanshi cikin damuwa. da sauri ya isa wurinta,"umma lafiya?"ta dube shi "ina fa lafiya,ummi ce tunda tayi sallar isha'i ta fice kusan awa guda zance jiya ka mata dukan fita wasan dare?" Abba yace "to wai me za'a yi wa ummi ne ta zama irin sauran yara?" umma tace,"addu'a ce Abba,kuma muna yi kullum." ya juya cikin bacin rai,layin su Amina kawarta ya nufa,don bata wuce can.duk da cewa Amina bata kaita rashin ji ba. can din kuwa ya sameta,ta tara zugan yayan layi sai tsokanar

fada suke yi,ita ce shugaba. wata falwaya Abba ya samu ya jingina yana kallonsu,don yana iya tunkararta su diba da gudu. shi kam ba za ya iya guje-gujen nan ba,duk wanda yazo wucewa sai sun tsokane shi,wani su jefe shi,wani kasa zasu watsa masa su gudu wani kuma rigarsa zasu ja. c can wani shida budurwarsa sun zo wucewa ta fizge ledar hannunsu ta watsar,sannan suka ruga da gudu. tayo gurin da Abba ke tsaye bata zaci da mutum a gurin ba,sai dai taji anyi caraf da ita.sai da Abba ya zabga mata koso a tsakiyar kai har tayi fitsarin wuya,sannan ya tasata har gurin mutumin data yaga ma ledar. suna tsugunne suna tsintar lemunsu da ayaba ya ce,"malam ga wadda ta yaga muku leda." da zafin nama mutumin ya mike,Abba ya ce,"gata"mutumin ya shakota yace yau sai naga ubanki." Abba ya ce,"ko kara ka kai gidansu nine zan hukuntata,don haka gata na kawo maka kanwata ce kuma naga lokacin data tsokaneka." jikin mutumin yayi sanyi ya ce,"na gode bawan Allah,taje taci albarkacinka." Abba yace "daka nade ta." mutumin yace,"ba komai,ke kuma ki canza hali ke mace ce." Abba yace nagode" sannan ya tasa ta zuwa gida. Bokiti ya cika da ruwa ya dora mata,,umma rasa bakin magana tayi daya sanar da ita tsokanar daya tarar da ummi suna yi. Daga karshe ta ce,"Allah ya shiryaki,abind ya sameki kada ya sami sauran dangi. Alhaji kuwa daya sameta dauke da bokitin tana kuka tana fadin "yaya Abba na tuba,bazan sake ba." ya ce,"uwata bakya ji ne fatan Allah yashirye ki."ya nufi dakinshi.tsohuwa takaicin Abba ne ya hanata fitowa tayi magana. nata ganin,ummi bata wuce fita tayi wasa da kawayenta ba,a cewarta ba laifi ba ne. amma an bi an tsangwami yarinya,an hanata walawa.sai da Abba ya gaji dan kanshi sannan ya sauke mata ruwan. Sannan ya mammaka mata takalmi,sannan ta shige dakin tsohuwa.tsohuwana daga kwance ta dubeta. "yaga dama ya kyaleki?kai mai sunan malam akwai mugunta.zo ki kwanta." cikin kuka ummi

tace,"kayana sun jike,bokitin ruwa fa ya dora min."tsohuwa tace,"barshi da halinsa,ace mutum ba zai sake ba?" ummi tace,"ai sai na rama,shima din sai yayi kuka."tsohuwa ta ce,"a'a,kada ki soma zancen ramakon nan.kin san ko kin rama ke ce zaki kwan ciki." ummi ta ce,nifa sai na rama."tsohuwa ta ce,"baki gaji da shan wahala ba kema da shegiyar gaddama,ga zanina nan kikin raki ciro ki daura kizo ki kwanta." ummi tayi lamo bayan tsohuwa tana tunanin dame zata rama abinda Abba yayi mata jiya.har bacci yayi gaba da ita waiwaye............ SULAIMAN shine asalin sunan Alhaji babba,Aminu kuma shine Alhaji karami. tsohuwa itace mahaifiyar su,kuma su kadai ne yayan data haifa.Asalinsu yan zamfara ne a kauyen daji a karamar hukumar kauran-namoda. malam Idris mahaifinsu shine ke zuwa yawon fatauci,har Allah ya zaunar dashi a garin kano,da matarshi Habiba. sunzo da yayansu guda biyu,sulaiman da Aminu.sun yi karatun muhammadiyya mai zurfi,amma basuyi karatun boko ba. sannan ya dora sukan harkar kasuwanci,Allahya albarkaci kasuwancin Sulaiman inda harkoki suka bude mishi cikin kankanin lokaci. matsalar shi daya rashin boko,malam idrisu mahaifinsu yana daya daga cikin wadanda basu amshi boko ba lokacin da tazo. Don haka sam bai saka yayansa ba.Sulaiman ya auri Suwaiba wadda suka dauki watanni suna soyayyya,ita yar unguwar sheka makaranta ce. Amma asalinsu yan Daura ne jihar Katsina.kafin aurensu sai da yayi gini a unguwa uku gidaje guda biyu iri daya. Ya ce Aminu kaninsa ya zabi gida duk da cewa a lokacin baiyi auren ba,wannan abu yayi wa mahaifisu dadi. yayi ta shiwa Sulaiman albarka,don haka sai aka rufe na Aminu,yayin da sulaiman ya tare a nasa da matarsa Suwaiba. / ZURFIN CIKI book 1 part 2

ZURFIN CIKI book 1 part 2

Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 21:40

Kwanci tashi 5yrs ta miqa suwaiba bata taba ko batan wata ba. awannan yr ne mahaifinsu ya cimma 1yr da rasuwa. saida aka watse makoki

danginsu na qauran-namoda suka koma. sannan sulaiman yace da aminu, to ni xan dauki tsohuwa in maida ta gidana,kai kuma aminu ka fito da mata kayi aurenka dan mu xauna kusa da juna. tsohuwa ta saka kuka tace wannan yaran nidai da ka barni na xauna da gidan xai xama kufai. sulaiman yace tsohuwa kiyi haquri, sai a saka haya.aminu yace haka xa ayi. daqar tsohuwa ta yarda dan tace ita wannan gidan mutuwane xata rabata dashi, dan gidane me tsohon tarihi a gurinta. ta ce gidan da mijinta ya rasu gidan da ya kawo ta tun tanada jajayen sawunta. suka dai lallabata. Ikcn da aminu ya gabatar da sahura a matsayin matan da xai aura, tsohuwa ta tuma ta ce ba ta laminta ba, don kuwa kowa yasan mahaifiyar sahura gun masifa. sanna sahurace ta gajeta. aminu sai ya watsar da mgnn auran gabaki daya har tsawan Ikc. sulaiman yanata roqan tsohuwa ta amince, dan ya lura aminu yayi nisa. Ba yadda tsohuwa ta iya, dole ta amince, aka sha biki ta tare gidan aminu. mai hali dai baya fasawa, dan sahura batasan hulda da suwaiba da surukarta, gashi daga kawota ko 2mth bata yiba ta kama fada da yan unguwa. a cikin 3yrs sahura aka samu ciki. Ikcn sulaiman ya samu xiyarta qasa mai tsarki shida tsohuwa dan sauke farali. sunyi addu'a allah ya bashi xuri'a shida aminu.suna durowa gida suka samu Ibrn cikin sahura, murna a gun sulaiman tamkar matanshi ne keda cikin.Ikcn haihuwa tahaifi da namiji murna gun yan uwa biyu ba'a magana, anyi shagalin suna inda yaro yaci sunnan mahai finsu wato idris shine suke kiranshi abba. Sannan Ahaji Sulaiman ya biyama qaninshi kugeran makka daga nan ne aka samu ahj Babba da ahj qarami tun abba yana jariri ahj babba da matanshi suke dawainiya dashi Sahura ba taso saidai ba yan da xaitai da ita. domin alj qarami na gama shirin fita xai saba shi sai gidan sai yayi kukan nono ake maida shi, saidai tayi ta mitar cewa anriqe mata yaro gidan,sahura dai in an kawoshi bata isa taxoba dan tasan tsohuwa tafita danja.duk da gugar xana da haibaici da

sahura take antayo ma suwaiba ta katanga ko inta je gidan, baisa ta daina dawainiya da abba ba. cikin hakane sahura wata ran sahura ta tashi da xaxxabi mai tsanani da amai, shine taje asibiti ganin likita ya tabbatar mata da tana dauke da ciki.ko da ta fadama alj qarami ba qaramin murra yayi ba ita kuma ta batarai, yace tunda abba yana tafiyan shi ko ina ayaye shi. Da yamma bayan yadawo kasuwa ya shiga gaida tsohuwa shine yake gayamata xa'a yaye abba. tace saboda me? ku barshi yayi 2yrs. sai yace ai uwan tanada juna biyune, shi yasa, daman sha waran da nakesan fada maki shine xanba yaya shi kyauta har abada.tsohuwa tace kai amma ka kyauta. Washegari da safe shine ma yayi ma abba wanka tana kwance ya shirya shi, sannan yace mata ta hada kayanshi duka dan xan kaishi gidan ahj babba gaba daya. tace kana nufin kayi kyauta dashi gaba daya? yace ea. tace tabdi!,ba xai yiwu ba. infishari banxane kaxa tayi mana. su wa yace kada su dage su samu nasu dan? nima wahala nasha na haifi dan, ba shago na bude ya fito ba....sam bai kulata ba, ya hada kayan yaran ya fita. ya shiga gidan ahj babba da shi. dakin tsohuwa ya shiga, nan ya samu ahj babba suna gaisawa, yace yauwa, dama gurinka naxo yaya. abba ya sauka daga jikin babansa yaje jikin ahj babba da gudu, ahj ya dauke shi ya rungume. Ahj qarami ya keqa ya kira suwaiba,ta shigo ta xauna sai ahj qarami ya soma jawabi da cewa. tsohuwa ina san ki xama sheda, yaran nan na ba yaya da suwaiba har abada.ahj babba yasake rungume yaran a jikinshi wani saban son shi ya ratsa shi. idanshi suka kawo qwalla, suwaiba ta sa kuka tace mun gode da wanna abu da ka yi mana. Allah ya bamu ikon riqeshi da amana. ahj babba yace bani da bakin da xan maka godiya, saidai ince allah ya qara xumunci. ahj qarami yace haba yaya dana nakane, saidai inasan abba ya xama xaka kai daya. tsohuwa tace allah ya maku albarka daku da yayanku, kaima allah ya baka haihuwa. sukace amin. Sahura kuwa mijinta na fita da yaro, itama ta xari hijabi ta nufi gidan

iyayanta, ta shaida ma mamanta cewan aminu yayi kyauta da danta, kuma yaba mutanan da basa qaunan ta. nan da nan uwar tahau masifar cewan ba xai yuyu ba, ai dole ya baki danki. shiko uban cewa yayi ai ikon sane, dan haka baiga laifinsa ba dan yaba dan uwansa dansa. sannan yace ,ta tashi ta koma. uwar tace ba xata koma ba, ya ce ta xauna. bai sake bi ta kansu ba, ya ci gaba da harkokinsa. shiko ahj qarami cewa yayi baxai bita ba, lokacin da ya dawo ya samu batanan, sannan bai fadama dan uwansa ba har aka kwana. sukuma su suwaiba basu fahinci sahura batanan ba dan ba hurda suke ba, saida kukaxo cin abinki ahj qarami bai futo da kwanu ba. sannan wan yace iyalin naka bata nanne? yace yaji tayi, niko baxan bita ba. ahj babba yace akan wani dalili ne? ahj qarami yace ban sani ba, na dawo gida ban ganta ba. da safe ahj babba ya tashi gaba sukaje gidan, sahura ba kunya tace danta takesan ya dawo mata dashi, inhar yana san xama da ita. Ahj babba yace, indai danta ne xai maido shi. ahj qarami yace shi kuma inhar sai an dawo da dan to ya haqura da auranta. kuma na cikin ta ma inta haife shi xaixo ya ansa ya qarama wansa inya so yaga yadda xatayi. duk juyin da akayi yaqi yarda daga qarshe ma tafiyan shi yayi. ubanta yace da ahj babba kaima jeka yadda suka so haka xasu yi. satinta guda taka abincin kirki gagaranta yake yi, ita kuma uwan ta daina samun wani abu daga gun sahurar ke kawo mata. dan haka suka yanke shawaran ta koma, duk da haka saida ya shareta na kwana uku sannan ya sakar mata. haka ta haqura saidai tasha alwashin dun runtsi sai danta ya dawo hannunta. sannan ta kulla sabuwan gaba da ahj babba da suwaiba kuma tace duk tsohuwa ce takitsa abin. abba yana samun kulawa tare da tarbiya mai kyau.sahura ta haihu ta sake samun da namiji aka samasa bashir, daga nan haihuwa akai akai.. Tun abba yana qarami ya koyi wasu halaiya na ahj babba. da farko, sallar asuba,axahar, laasar, magrib da isha. ahj babba kan tasa abba suje masallaci da rana kuma

umman sane ke turashi. ranan jumaa ahj na dawowa gida dan ya tafi dashi. dan haka sallah ta xauna ma abba da xaran lkc yayi xai fara shiri yi. sannan ya iya sadaka dan dasunje yana bashi kudi ya rabama almajirai ko yasa a asusun masallaci. sai xumunci aduk lkcn da ahj babba xashi xanfara yana tafiya da shi. ya tashi da san iyayan shi matuqa bai taba sanin basu suka haife shi ba. duk da cewan duk lkc da ya shiga gidansu umman bashi takan cemai bafa umman kace ta haifeka ba, nice na haifeka. riqonka muka basu. in yaji haka sai yace allah kiyaye. sai ya baro gidan ita kuma taita xakinsa. inya fadama umman shi saitai murmushi ta rungume shi. ya ce aidai kece ummata ko? ita kuma tace nice ummanka rabuda ita kaji. abba yanada tausayi dan haka ya taimaka ma ummanshi aikin gida. shekara sha biyu ya sauke kur'ani.a lkcn ne ya gama pry ya samu xuwa js1 Abba makarantan masu kudi ya ke yi.ita kuma sahura duk yaranta ta batasu, musamman bashir. duk lkcn da akace yaje makaranta inyace ya gaji, saitace ya xauna kaje gobe. ko ahj babba ya korashi sai dai ya labe inya tafi shi kuma ya dawo. yafi san xuwa qwallo ko shagon game. to hakama qannansa duk sun dau irin tarbiyyan uwarsu. cikin haka wata ran umman abba ta tashi da matsananciyan mura, lkcn ahj babba yaje legos don taho da kaya. ahj qarami ne yakaita asibiti bayan gwaje gwaje, an gano ciki wata biyu da yan kwanaki. murna gun ahj qarami tamkar yayi tsuntsuwa yaaje ikko ya fadama ahj babba. suna isowa ya shiga gun tsohuwa ya sanar da ita. nan take tasa kukan murna.ita kuwa suwaiba tamkar mafarki, sai kunya ta isheta. lkcn da ahj qarami ya fadama sahura, sai cewa tayi um, bana an tabuka, ni dai gani da cikin na shida amma sai yauxu ta samu daya. ahj qarami yace kinji matsalanki, ke ba dai kiji wani ya samu qaruwa ki taya shi murna ba, sai dai baqin ciki. ta ja tsaki bakin cikin me xanyi? tunda ni ga nawan. ciki mai laulayi suwaiba ta samu, wanda duk abin da taci sai ya dawo. wannan lamari ya daga ma ahj babba

hankali da abba, duk aikin gidan abba ke yi, ga makaranta, ko an hanashi sai yayi.dan haka aka dauko harira qanwar suwaiba, wanda mijinta ya mutu. umman abba dai bata samu kanta ba saida cikin yayi wata biyar. sannan ta samu sauki.lkcn sahura tanada cikin wata bakwai, lkcn haihuwa ta haifa mace, murna gurinta kamarme, dan sai yanxu ta samu mace. safiyar talata umma ta tashi da naquda, hankalin ahj da abba ya tashi matuqa. duk da tsohuwa tana ta kwantar masu da hankali, ranan abba ko makaranta bai jeba, duk da san makarantansa, har suka dawo sallan axahar shuru. ahj babba yace tsohuwa bari na samo mota akaita asibiti. tace to. yana fita ba jimawa ta haihu. ta santalo yarta mace mai matuqan kama da ahj babba. tsohuwa tace da abba,mai sunan mlm bi su ahj kace sudawo ta haihu. dama harira tasa ruwan wanka lkcn da suka xo ta fito daga wanka.nan aka wanke yarinya yan barka sai xuwa suke amma sahura saida aka. Sahura saida aka kwana sannan ta shigo. ta dauki yar ta taba baki tace wannan yar baqinqirin haka sai idanu daqwa daqwa. wata mata da taxo barka tace ai wannan yar sak abba,suna kama sosai. sahura ko kunya ta ce basa wani kama da abba. da tasamu kyan abba da tayi kyau, umma tayi ma matan alama da haunu tai shuru. ranan suna taci sunan tsohuwa, wato habiba, dan haka umma ke ce mata ummi. abba yana ji da ita, saidai in yanasan tsoka nanta sai yace dubeta ta ba ummata wahala, sai na xaneki kika girma kika qi mata aiki. umma taita masu dariya. tsohuwa ma naji da ita dan guta take wuni. tunda ga kan ummi umma bata qara haihuwa ba. abba yana aji uku suna qoqarin xana (j.s.c.e)ya dage sai ahj ya saka shi shagon dinki. ahj yace abba kabar batun dinkinnan ka tsaya a karatunka. yace ahj nidai ina so kaga inna iya su umma sun huta dakai dinkin su gidan laminde. umma tace ka barshi yayi ahj sana an hannu ai tanada dadi, kaga in ya gama bokon ba bai samu aiki ba xaya riqe kanshi da sana anshi. ahj yace to shi ke nan Ahj yace, to shi kenan, wane shago

ka ke san shiga inkai ka? yace, na can bakin titin nan, in da kake saya na lemo. ahj yace shi kenan. mafarin shigar abba gurin koyan sanaa kenan. ummi ta taso da rigima, tsiwa tare da tsokana, wanda yasa suka daina shiri da abba sam. abba ne ya kaita makarantan boka da islamiya, kullum yaje daukota sai ya raba fada ko ya bada hakuri. umma kullum addua take fili da xuciya da lokutan sallah, allah ya shirya mata ummi. ita kuma tata kalan quruci yan kenan inta girma xata daina. tsohuwa takance aini me sunana kingama min komai, domin banasan ragon da, da in kai qara gara akawo min na bada haquri. duk lkcn da tayi wannan kalman sai sunyi fada da abba, dan cewa yake ai dama tsohuwan nan tuni na ane kin daure mata gindin ta siqa tsokanan yayan mutane. ita fa mace ce ba namiji ba, shi kenan bata da aiki sai dambe? tsohuwa takance batta tayi. tunda ganan abba basa shiri da tsohuwa. ita kuma fati yar sahura kamar ummace ta haifeta dan bata da hayani. ummi kuma kamar sahura ta haife ta. Wata rana abba ya ke cewa, umma da ace lkc daya kuka haihu da umman bashir, allah cewa xanyi kunyi canjin yaya. umma ta dube shi dan me kace haka? yace sbd masifar ummi irinna umman bashir ne, fati kuma ba ruwanta kamar ke.dariya kawai take yi. kwanci tashi ummi ta gama pry, lkcn abba yana shekaranshi ta qarshe a jamia. yana karantan (mass comm)ne dan yana san xama dan jarida. umma tasoshi da likita amma yace baida raayi. tace kaga kai bakada hayaniya abba aikin jarida na masu maganane. yayi murmushi yace umma kenan. ummi ta samu shiga aji daya a qaramar sakandare. maimakon hankali abin nata sai gaba yakeyi. aduk lkcn da tai laifi abba ya daketa sai tayi wani abun dan tabashi haushi, da sunan ta rama. ahj babba ya bude mai shago, tare da xuba mishi kekuna. tsohuwa tace dakai wanine mai sunan mlm, saika tafi da takwarana ta koya. abba yace ko a kwafan shago na na ganta ba sai na karya mata qafa ba. ummi ta murguda baki, sai daya tafi sannan tace allah ya kiyaye inje wannan qaxamin

shagon nashi. Tsohuwa ta ce,"tafi can kema da baki son ci gaba, in banda abinki da zaki kwantar dakai ki koya in an tashi auranki basai a saya miki keken ba. in kuma shi kika aura kinga shikenan inya samo dinkin da yawa saiki taya shi, ta ce"Allah ya kiyaye me xanyi da yaya Abba,yayi ta cin xalina?ni bana son shi" Umma dake gefe tana jinsu ta ce,"ke in kin samu kamar Abban ma ai kinji dadi,shine zai ce mai zaiyi dake? mara hali irinki." Ummi dai tayi shiru tasan inta cika surutu kan Abba yanxun nan umma ta doddoketa,umma tafi son Abba fiye da ita. watan ramadan ya tsaya,duk daukacin musulmi sun dauki azumi ranar da akai na uku Abba ya shigo gida karfe daya saura. daga shago yake zaiyi wanka yaje makaranta don yanada darasi karfen biyun rana. Gidan shiru kowa na bacci,don haka bai shiga dakin umman shi ba don baya son ya tasheta ya shige bandaki. Da ya gama ya fito ya nufi daki kamar ance ya kalli madafi, ummi ce tsugunne tana cin abinci. ya tsaya yana kallonta, dagowan da xatayi suka hada ido, yace ke! karya axumin kika yi? ta toshe bakinta sannan nace dan allah yaya kayi haquri. yace fito muje. ya kaita dakinshi yasata gwale gwale. da xashi masallaci ya kulleta ta baya. ya ce inyaso ki tashi kafin na dawo, xan gane. yana fita tahau binci ken abinda xata lalata mashi. ta ciro bidiyon da yake kallo xata doka da qasa, sai taga kwalin wani kaset tana kallon hoton jikin kwali, na tsiraici ne. ta xare ido kicin mamaki, tace lalle yaya abba, daman shi dan iskane? to kuwa xan tona mai asiri. ta turashi cikin xaninta, da taji motsin shi yana bude qofa sai ta koma inda take. ya shigo ya kalle ta ya ce nasan kin xauna dan kinga bananan. ya xauna bakin katifa, sannan ya dubeta fuska daure. ummi meyasa kika karya axumi? tace ba komai. yace tunda aka fara axumi kike karyawa ko? tace yaune kawai yaya abba. yace kinsan hukuncin wanda ya kasya axumi da gangan. Tace eh an fada mana a islamiya, amma mlm yace sai wadanda axumi ya wajaba akan su. ya kalle ta cike da mama ki, a xuciyanshi yana

cewa, yanxu har yarinyan nan tasan akwai wadanda axumi ya wajaba akansu? afili kuma yace lalle ummi kina buqatan sa ido. dama saboda bai wajaba akanki ba shiyasa kika karya? to daga yau xansa maki ido, kuma xan fadama umma ta sa maki ido. hakanan duk wani abu da akeyi lkcn axumi an daina qyale ki, xaki ringa sallar tarawi, ke har tahajjud sai kinyi shi. sannan bayan axumi saikin rama wannan axumin. ya xuba mata ranqwashi a tsakiyan kanta ,tare da cewa tashi ki fita munafuka. daga dakinshi bayi ta shige ta qara kallon kwalin, sannan ta maida ta soke shi, tace sai na tona maka asiri. da dare bayan angama bude baki, abba xai tafi tarawi ya shigo dakin umma yace ina ummi? umma tace gatanan kan kujera tayi sharkaf, wai yau taji axumi. abba ya shiga ciki yana kallanta. yace umma xaki yaudara ko yar rainin wayau, tafa karya axumi daxu da rana na ganta tana cin shinkafa. Yace shine kika xube wai ke kin sha wuyan axumi ko? umma ta dube ta tana mamaki, tace abincin da kike kinba almajirai da ma qarya ne? ya dubeta yace biyu kenan ga larya axumi ga qarya, xaki sani. tashi muje salla ko in ballaki. umma tace allah ya shiryi halinki. abba yayi dariya tare da cewa, kema dai umma yaxaki amince da batun wai tac almajirai abinci, su basa axumi ne, umma tace tunanin haka sam bai xo min ba. saida ya sakata sahun salla, sannan ya nufi gun maxa. bayan ya gargadeta da cewa in an idar ta jira shi, inyaxo batanan sai ta sani. koda aka idar da yaxo bata nan gurin ya kaure da dambe da wata yarinya wai da suna sallah tana bigeta. shine daga idarwa ta cakume yarinyan da fada. bai tsaya saurarantan ba ya cire ta kalmi ya shiga dukanta, sannan ya tasata xuwa gida. sai da ta shige dakin tsohuwa sanna ya koma nashi dakin. hakanan suka ta xuwa masallaci har axumi yakai ashirin. Ahj ya kawo masu shadda da leshi da atamfa na sallah ita da umman su bashir da fati. ya suya masu takalma da mayafai, abbane xai masu dinki, ran ummi baya son dinkin abba, domin wanda take so bashi yake mata ba.

ta ce umma dan allah nidai a bani dinkina na kaima laminde, yaya abba baya min ne kyau. umma tace kije ki karbo da kanki. tace ai baxai bani ba ne, xai dakeni. umma tace ai nafi san ya dake kin, lamindan finshi dinki mai kyau tayi ne? ummi tace nidai gara ita. tsohuwa tace ai banga lkcn da mai sunan mlm xai faranta ma takwara ba, kullun burinshi ya quntata mata. umma tace tsohuwa ummi fa ba a mata gwaninta, inace dinki in yayi mata har aro ake xuwa yi? ta dube ta tace keda shine inya jiki kyayi biyu babu, yaqi maki dinkin luma ya hana kayan bare kiba laminde inga ta tsiya. qarfe dayan dare ya tura dakin tsohuwa tana xaune a kan sallaya tana addua, abba yayi murmushi. tsohuwannan kina birgeni dama kina ibadan dare? ya kalla kan gadonta, ummi taya dai dai tana ta bacci./ ZURFIN CIKI book 1 part 3 ZURFIN CIKI book 1 part 3 Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 21:42 Ya kalla kan gadonta, ummi taya dai dai tana ta bacci. Yace, ummi ke! ummi!! tashi. tsohuwa tana yi masa alama da hannu gami da gyaran murya, wai ya bar ummi maimakon haka ma sai ya dauki wani kofi nan gefansa da guntun ruwa a ciki ya watsa mata a fuska. ta farka firgigit, yace taso, da sauri ta tashi yace dauko hija binki maxa. ta dauka suna fita tsohuwa tana sallamewa. tace kai mai sunan mlm ka lafama yarinyan nan haka, wai axumi wajaba akanta yayi da xaka tasheta da tsohon darannan xuwa masallaci? yace kema in xaki, xo muje. ya tasata suna tafiya tana hada hanya suka tafi tahajjud. sai qarfe hudu na asuba aka tashi. ummi har kuka tayi saboda tsananinjin bacci, amma tana tsoran kar ta kama bacci yaxo ya same ta. tun tana layin bacci har ta gyagije. sakamakon tashinta da matan kusa da ita keyi. kafin kwana uku ta saba da sallan dare, lkc nayi xata farka. abba yana xaune ga dinki gabanshi amma yana can tunanin bushira, yarinyan da yake matuqan so ce. amma yana shakkan fada mata,dan iyayanta sunada kudu matuqa. kuma shine yakema duk yan gidansu dinki. Ahmad abokinshi da ke gefe kuma sai yayi murmushi, yasan tunanin bushiqa ne ke damun sa, dan haka sai ya ce, abba kasan allah, abari ya huce shi ke kawo raban wani. haka kuma ZURFIN KICI, ba xai kai ka gaci ba. ka fada mata kawai. abba ya ce hum ,ina tsoron kada ta ce bata sona, dan bansan ina xansa raina ba. ahmad yace daga ganin yadda take jin kunyanka tana sanka. abba ya kalli ledan da ke dauke da dunkunan su bushiran, yace ina xatan yau xasuxo amsan kayansu, dan tun jiya nace suxo.ahmad yace to in sunxo kayi qoqari ka fada mata mana, indai ba ragon namiji kake ba. abba ya tsurama qasa ido yana tunanin in sunxo mai ce mata? kusan awa biyu sukaje sukai sallan axahar, tungan motan ta tsaya yasan tasu bushurane. shi kadaine a shagon sauran basu dawo ba. bushura ta shigo da qannansu da yarsu aisha. ya taresu da faraa, suka gaisa kan bushura na qasa, sam bata iya kallan abba tela kamar yadda suke kiranshi. Ya tura masu kayansu suka duba sunata murna dan ya masu wadda sukeso. aisha ta aje masa cikon kudinsa kan table. har sun fita yagadai baxai iya hakuri ba, yace bushura xo gashi. ta juyo tana dariya taxo. yace bushura inasan na fada maki wata magana gashi kuna sauri ko? ta kalli motan tace fada min. yace kina sona? ta

xare ido sannan ta ruga da gudu. gabanshi na faduwa, bata tsaya ba sai mota. ya kwantan da kanshi akan keken yace menene maanan gudun da yarinyannan tayi? ya tambayi kansa, qarfe uku sunada lecture, amma baya xatan xashi makarantan. ahmad ya dubi abba wanda daga ka dube shi xakasan yana kin damuwa. yace wai banaga sunxo ba? ko ba motan su bane? shiya bandawo ba nakuma hana yaran dawowa dan ku sasanta. abba yace um, inaga yarinyannan gara na haqura, dan bana san insa kaina cikin tunani. ahmad yace ban gane ba, abba yace, to naga daga tambaya tana sona, saita kwasa da gudu ta shige mota. ahmad yayi yar dariya sannan yace ,amsan ta baka. tana nufin tana sonka. abba ya harare shi kada ka maidani dan iska, ina ta magana ta xabga da gudune shine tana sona? yace jeka tambayi manya .yaci gaba da cewa kaine baka mata magana da hikimaba, ka fito mata kai tsaye baka sakaya ba. abba yace, kai nifa ka sanni ba ruwana da wata kwana kwana, idan abu yayi min bana kwana, inko bai min bama haka, ni ba ruwana. Ahmad yace sai xurfin kici ko? da ya aka shawo kanka ka fada mata,abba ya mike tare da kallan agogo, yace inada lecture. gida ya nufa dan shirin xuwa makaranta, har yayi kamar ya tambayi ummanshi cewa in ka ce ma mace kana sonta taji kunya ta gudu wai alamun so ne? sai kuma ya kasa, yana jin nauyi amma in bai samu wata manufa ba dole yaxo ya tanbaye ta dan baya boye mata komai.bushura yar ahj sale ce kwamishinan gona na wannan xamani, gidansu yana karkasara. danqareran gida ne ginin xamani, sun san abba ne sanadin dinki da yayi wa wata qawansu jamila.dinkin yayi matuqan birge su dan haka suka fara kawo masa dinki, tun ranan da ya fara ganin su bushura ta kwanta mashi a rai. to ashe ita ma yamata.shiyasa yau daya furta mata take ganin kamar anmata gafara da aljanna.wata xuciyar tace ,to yanxu da kika gudu in ya xaci baki sansane fa, nan take hankalinta ya tashi har tana rayawa ga abba can da wata.dan haka taga dolene ta koma gun sa inhar tana sansa. dan tasha ganin mata na masa tayin kansu in sunxo kawo dinki.nan ta soma tunanin wace dabara ce xatayi ta fita?saiko ta warware daya siket din kayanta cikin dare.da safe ta nunama momynsu tace mata telan ya manta bai hada wannanba,dama yace xai gwada nine kafin ya hada.momy tace direba ne xai kai mashi.bushura tace momx xaifa gwadani ne muje dai xa kaini.tace to kuje, bushura ta danyi gayunta suka tafi.saidai kash! bata samu abba ba ance mata yana gida. tace gidan da nisane, aka ce mata babu nisa,dan haka ta sa aka rakata.tacema direbansu tana xuwa telan na gida.gidan ba nisa. A qofar gidan su abba ta tsaya, sai ga ummi ta sheqo da gudu tana dawowa daga aike.ta tsaya tana kallan bushura, sannan tace lafiya?bushura ta dubeta. yauwa abba yana nan?budan bakin ummi sai tace yaje kashi ya fada a masai.bushura ta dafe qirji, yaushe? ummi tace oho.sai ga abba ya futo sanye cikin shadda bulu mai duhu yana ta qamshin turare.shawara ya yanke lkcn da yake xaune a shago kan cewa yaje gidan su bushura,tunda gidan kwamishina ba boyayye bane,suka hada ido da bushura,ta saki faraa sannan ta dubi ummi,kince ya fada ina? ummi tayi ciki da gudu.ya bita da kallo sannan ya kalla bishira,me tace maki?bishira tace, ba komai.saidai dariya da maganan ummin tabata.yace tunda baxaki fada min ba xomuje ki gaida ummana.cikin muryan jan hankali tace ina jin kunya.ta bude jakanta tace kamanta baka dinke wannan siket dinba.yace mugani,yaga yadda aka warware shi aka cire xaran da kyau. murmushi yayi dan yasan ya dinka siket din,kusan shinema na farkon dinki.ya gane yaran nata qila san ganinshi take san yi. Ya dinke siket din yana cewa"to amma sai dai ayi min izini inzo gida in kawo da kaina in na gama." tace haba dai,ya za ayi in taso ka?"ya ce,"ba komai,in dai anyi min izini sai inzo," ta ce,"to in maka kwatance?" ya ce,"a'a huta kada ki bata bakinki,nasan gidanku zanzo anjima bayan

tarawih." ta ce,"to." sai mun zo" tace"ku dawa? ya ce,"abokina mana,kinga zo muje gurin ummana ku gaisa." Bishira ta bishi cikin jin kunya.tun kafin su shigo daman ummi ta shiga gurin umman da gudu tace mata"umma ga budurwar yaya Abba." Umma tace budurwa kuma? tace eh ai zama su shigo.daga nan ta kara kyallawa dakin tsohuwa tana fada mata. Umma dai jim tayi dan bata da wani burin da ya wuce ta baiwa Abba ummi,kuma da tasan har zai ga wata can da wuri haka data fada masa kudurinta,sa tay 'ZURFIN CIKI' gami da nauyin baki....... sallamar Abba ce ta katse ta ta ce,"shigo Abba." ya ce Umma bakuwa ce taxo gaisheki.Umma ta fadada fara'arta tace to shigo,ba dai surukar tawa bace?" ya ce,"ai ita ce kam" Bishira ta shigo tana sunne kai,ta gaida umma Umma ta ce,"masha Allah,Allah yasa rabon muce."Abba yana dariya ya ce,amin ummana."ya dubeta,"tashi ki gaida kakata." suka nufi dakin tsohuwa,umma ta jinjina kai .tabbas Abba nason yarinyar,in ta dubi yanda yake fara'a da zumudi. a fili ta ce,"Allah yayi mana zabin alkairi."ummi na kwance kanta na cinyar tsohuwa,sai ta kalli bishira ta tuntsure da dariya,lokacin da suke gaisawa da tsohuwa. Abba ya ce,"dariyar uban me kike yi?" sai ko ummi ta sake shekewa da dariya. ya nufota ya suri kafafunta,tsohuwa ta ce haba mai sunan malam yanxu in bata yi dariya ba kuka zatayi?" ya ce,Bishira tashi muje" Tsohuwa tace to yanmata mun gode ki gaida magabatan naki,sannan kiyi ta hakuri da halin wannan miskilin." Umma ta ce,"tsohuwa kodai kishi ne?suka yi sallama,ummi wadda tunda ya shureta ta rigasu fita sai ta dauki takalmi Bishiran guda daya takai soro (zaure). don haka da suka fito suka shiga nema ummi ta kule uwar dakin umma tana ta dariya tana lekensu. Abba ya ce,"ummi! ummi!!" taki amsawa ya nufi waje da niyar dubota don yasan ita ce zata dauki takalmin,sai ga takalmi a kofar shi. Don haka ya dauko kawai ya dawo ya bata umma ta ce,"ka kaita su gaisa da umman Bashir." Abba ya ce,"a'a ba yau ba."ya rakata wurin direbansu,kusa da shagonshi sukayi sallama da alkawarin zai zo washegari. yaje kuma bishira ta fada masa lallai tana sonsa sai dai tana tunanin iyayenta ko zasu amince? ya ce,to shi dai zai turo magabatansa su nemar masa izinin zuwa zance kamar yanda yake a shari'a Bishira tace a'a ya bari tunda yanxu shekarar farko take a babbar sakandare(s.s.1)ba za a bari ya dinga zuwa ba,amma zasu dinga haduwa gidan yarta dake na'ibawa. Abba baida zabin da ya wuce ya yarda da hakan tunda tace baza a barta yin tadin ba.sai dai fargabar shi kada nan gaba sunyi zurfi cikin soyayya ace ba za'a bashi ba. ta ce,"Babana bashi da matsala,amma momy dinmu ce abin tunani."Abba ya ce,"shikenan Allah ya shige mana gaba." soyayya ce mai karfi ta kullu tsakanin Abba da bishira,wanda har ummanshi da kanta tasan cewa Abba yana son yarinyar. Domin duk lokacin da zaije gurinta tana lura da zumudin da yakeyi,kazalikain tace ka gaida surukar tawa, bakinsa baya rufuwa. Don haka sai ta tattara batun ummi ta aje a gefe addu'a ce kadai bata daina ba.ana sauran kwana uku sallah.Abba ya siyo fenti yazo da mai fentin nana ak fente gidansu ciki da bai. Da yamma kuma ya kawo dinkunan su ummi da fati,ummi tasa ihu,sam irin dinkin da ta aro gurin kawarta Amina ba shi yayi mata ba,ya zai mata dink iri daya da fati? ya ce,"kin isa ki sani in miki dinkin da kike so?ta ce to ni dai bazan sa ba umma ta rafka salati tana kallon ummi ta ce,"ummi kina da hankali kuwa? kudi kika biya ko ko Abban sa'anki ne?" tace cikin kuka to ni umma ya zai min iri daya da fati? ya dubeta a fusace,"in kin bari na dauki kayannan wallahi bazaki sasu ba." Umma ta ce,"ni da zaka daukesu ma da naso"tsohuwa ta fito ta ce,"saboda me? akan wane dalili zaka amsar mata kaya?tunda baka mata wanda take so ba sai ka kyaleta." Da hannu Umma tayi mishi alamar yayi shiru,sannan ya fita waje.Abba ya kada kai ya fita. washe gari kuma ya shiga da me fenti har cikin gidan Alhaji karami,sahura tana daki lokacin da yake nuna

ma mai fenti guraren da zaya fara. Ta fito daga daki ganin Abba sai ta hade rai sannan ta ce,"mune kashin baya? ai dama ka bar shi tunda baka mai da mu wani abu ba,mu ne dai baka so din mahaifanka. Ta dalilinmu zaka shiga aljanna,ba dalilin wasu banzaye ba da sauri ya nufi hanyar fita waje don baya son yaji zagin da zata yiwa Alhaji da Ummanshi. wannan na cikin dalilin dayasa baya son zuwa gidan Alhaji Babba da Umma,sune suka ci kashi da fitsarinsa. suka bashi tarbiya da ilmi,suka ci da shi suka shayar dashi.amma sam basa yi masa abinda umman Bashir ke masa. haihuwarsa ce kadai su Alhaji babba basu yi ba,sahura tana zuwa har shago tayi masa rashin mutunci,sannan ta ce ya bata kudi,ta ce ya ba bashir kudi ko ta aiko fati. Bai taba kin bata ba,amma duk da haka bai tsira daga zagin rashin mutunci ba.ta ce ya tare a gidan ummanshi komai nashike mata,wai da kuma sam ba haka bane. Umma bata taba tambayar shi sisi ba,haka nana duk lokacin da ya bata wani abu ko ya sai mata,sai tace ina na umman Bashir? kaje itama ka bata,in ko bashi da yawa ni naci girma ka bata. Ranar sallar idi kuwa ummi koda tayi wanka kin saka sabon kayanta tayi sai na bara. Lokacin da zasuje sallar idi,Abba ya fito daga wanka ya kalleta ina kayanki sabo? ta tura baki"ni baxan sa ba." Yace,"to zanga wanda zaki bi masallacin,kuma ki kara magana saina fasa bakinki."sai ta wuce kofar dakin tsohuwa,sannan ta ce,"to ai dai nima nasan hanya,kuma sai naje."ta fada dakin da gudu. ya bita bata san yaga tsohuwa lokacin da ta shiga wanka ba,bayan fitowarsa.don haka ya ritsa ta ya kwakkwada mata mari,sannan ya rike mata kunne. zan kara fada ki fada? ta ce,"a'a kayi hakuri." ya saketa ya wuce,ta zauna tana kuka. misalin karfe hudu na rana ,bishira ta iso shagon dinkin ita da direba,shagon a rufe.don haka ta ce su karasa gidan. Can dinma baya nan,amma sai ta fito ta shigj gidan dauke da tire babba cike da kuloli. cikin kunya ta gaida umma,ta kuma bada a aje masa.umma ta ce,"to ko ina Abba yayi? kila gidan su Ahmad yaje."umma ta ce,"ke uwar gudu ina yayanki?" ta ce,"nima na ganshi?" karar bude kofarshi suka ji,ta ce,"leka in shine kice yayi bakuwa.shine kuwa,jin cewa ga bishira ya shigo da zumudi. Umma tace ka kaita ta gaida umman bashir. yace to, ta fito ta tafi kicin ta bar masu dakin,ashe ummi tana uwar daki tana jinsu.ya ce,yanxun fa daga na'ibawa na ke,ina ta xumudi in ganki. tace,na xaci ba xa kaxo ba ne,nace bari inxo ni,dan baxan iya kai dare batare da idanuna sunganka ba.ummi ta toshe bakinta saboda dariyan da yakesan kufce mata,yace sai inga kamar bakya sona.bishira tace haba abba, in kace haka bakamin adalci ba.yace to wadannan kulolinfa me kika kawo min?ta ce bude ka gani.ya bude ya gani yace kai, lalle ashe ni dan gatankine? tace sosai ma.ya marairece murya yace to bani abincin a baki.ummi daga cikin dakin tace, la'ilaha illallahu.abba ya miqe da sauri.kafin ya ankara ummi tayi fitan bindiga tsakar gida tana fadin la'ilaha illallahu,dama yaya abba dan is....umma ta gwabe mata baki,bayan ta fito daga dakin ahj babba.ummi wadda inta s6a magana ko ana hanata sai ta kai aya.ta dafe baki,tace maci gaba da fadin,umma to kinji abinda yake ce mata ne? umma ta jefeta da takalmi tare da cewa,wai baxa kiyi min shuru ba? ummi tace,to fa cemata yayi xai bata abinci a baki,kuma daman xan nuna maki wani kaset da yake kallo. Abba ya riqe kai tare da cewa ummi in na kamaki xaki sani, kaset din wa kikaga ina kallo? tace na yan is....da gudu ya bita ,yayin da umma ta jefa mata murfin kwano,amma duk haka ko da ta fita waje saida tace masa sai na nuna ma ahj kwalin kaset din.take ya tuna da kwalin kaset din daya boye,wanda ya qwace a hannun bashir,kaset din tsiraici ne wanda laanannu sukayi.abba cikin takaici yace,kai ummi! kai ummi!! kinsan allah in kina wasa dani xa karyaki a banxa.ta ce to ba a dakinka na gani ba?yayi qwafa,allah ya sani ya tsani ummi kamar ya shaqeta ta mutu.sai ya samu kanshi da qin

komawa gidan,kunya da nauyin umma yake ji,yasan dai ba xata kama xancan ummi ba,amma yasan xuciya da xargi,qila xuciyanta ta xargi wani abu.bashir ya fito daga cikin gidan su abba yace,yauwa bashir shiga gidanmu kace bishira taxo. Bashir rai bace ya shiga,dan yana jin haushi ya amsar me kaset.ya shiga umma na qofar kicin xugun tana tunanin halin ummi.bashir yayi sallama umma ta amsa.yace,abba ne yace in kira bira ne ni yace ne?umma tace gatanan ciki,taxo bakin qofa ta kalli bishira kanta na qasa tana mamakin ummi.yarinyan sam bata ji.umma tace kixo yana kira awaje.cikin kunya ta fita, yace da bashir rakata gun ummanka su gaisa.bashir yayi fara,a antynace ke nan?abba yayi murmushi. bishira ta xauna gaban ummansu bashir suka gaisa. bashir yace,budurwan abba ce. sahura tace,yau kika taba xuwa nan unguwan? kanta na qasa tace, xuwana biyu kenan.ta kalli bashir tace kaji ko? amma shine ko a turo ta nan gidan.nina haifi abba amma an gaje min shi.tace yarinya duba nan.bishira ta dubeta,ta dafe qirjinta ni na haifi abba nine uwansa.matan gidan can mai gidana ya bada shi a gunta,da ubansa da maigidan dan wa da qani ne amma sun gaje shi.bani da ikon sashi ko hanashi amma sun mallakemin shi. da muryan tausayi take maganar. Bashir yace, umma indai ya aurota xamu samu sauqi.bishira tace kada ki damu, insha allah komai xai warware. tace, to yan nan na gode.fati ta shigo ta gaidata cikin nutsuwa, bishira tace wannan qanwansa ce? umma tace eh, ai su ga sakamakon mugunta nan sun haifi yar muguwa mara jin magan. bishira tace, kai yarinyar bata ji. fati ta ce abba ya ce kixo.sahura tace kinji ko? shifa ko nan gidan baya qaunan shigo wa.bishira ta miqe ta balle jaka ta ciro sabbim kudi yan ashirin ko irgawa bata yiba ta bata, tace kinsaya goro.sahura tace harda abin arxiki?to an gode.bashir yace antyna inane gidanku?tace karkasana gidan kwamishinan gona.bashir ya raxo ido, nako san gidan,lalle antyna ina qara gaisuwa.bishiratayi dariya.abba na tsaye suka fito,yace mata to ki tafi xanxo amjima. tace baka kaini dakinka ba.ya girgixa kai, bai dace ba wannan ba mutunci bane,sam bai kamace yar mutunci suna xuwa dakin samari ba. bishira tace danme? yace sharia bata amince ba, damin duk Ikcn da mutum biyu suka kebe,musamman mace da namuji. Abba yace na ukun su shedan ne. irin wannan yana haifar da xinace xinace a bayan qasa.tace hakane ta tafi.abba ya rakata har mota, bashir kuma tamkar maroqi, sai fadi yake allah ya tsare antina ki sauka lfy.bayan tafiyanta abba bai iya shiga gidan ba tunaninshi daya kada umma ta xargeshi.dan haka ya nufa gidansu ahmad.ya ba ahmad Ibrn abinda ya faru.dariya ahmad yayi tayi.yace kai amma wannan ummin taku yar dirama ce. abba yace cikin takaici yanxu kai har kaga abin dariya?yaja tsaki yace allah na tsana ummi, namata muguwan tsana. dubi wannan yarfin da tai mani. ahmad yace xata bari, wata ranama ko ance tayi watace sam batayi ba.abba yace taf wannan yarinyan dawuya in xata taba yin hankali, duk wanda ya aureta ya auran ma kanshi fitina.ahmad sai dry yakeyi. da magariba ya shiga gidan,cikin saa ya samu ummi tana cin abinci.nan take ya kama hannun ta har saida tayi yar qara, yace muje ki dauko min kwalin kaset din da kika dauka, Umma tace, Abba na soma tunanin yarinyar nan tan da aljanu da gaske. abba yace hakama alhaji qarami yace, amma fa anje babu kowa akanta. ya saki ummi bayan ya ranqwasheta. sannan ya ce, in kika sake yarda ki kaga wani abu a dakina kika dauka sai na balla ki. washegari abba ya tasa ummi ya nufi gurin masu ruqiyya, amma da aka mata babu kowa a kanta kamar yadda ya xata. ya dawo ya sanar da umma,umma tace na gode allah.halinta ne ita kuma irinta kenan? yace irinta kenan umma,baxata canxaba saidai muyi ta mata addua, soyayyan abba da bishira ta bunqara,har dangin abba sun san da batun,sahura duk tabaxa ma dangi.sanadiyyan maganan da tayi ma bushiran na cewa an rabata da daxta.

wata rana bishiran tace masa xata xo gaida ummanshi,yace to cikin xumudi sai tace, umman su bashir fa nake nufi, ba ance ita ce mamanka ba? abba ya ce inji wa? inji ummanka. abba yace sam, ummana ba xata fada miki ba sai dai ko ita umman bashir din. tabbas itace ta haifeni, amma ba itace ummana ba.tace dan me? nan take ya hada rai. Abba yace mata ba matsalanki bane, so ban so ki saka kanki ciki. nan take ta yarda da batun umman bashir.ta a mince qwarai umman da abba ke kira umman shine muguwa ce.kuma itace ta raba abba da umman shi.dan haka saita tsiri xuwa gun umman bashir, tare da yi mata kyauta.shiyasa suka saba sosai.duk xuwan da bishira xatayi sahura saita kukkushe umman abba, tare da yi mata sheri. dan kawai bishira ta tsaneta,kuma bata xuwa gunta koda taxo anguwan. abba bai taba sanin haka ba,ita kuma umma bata taba fadan mai ba, dan ummi ta taba fada mata cewan budurwan abba tana xuwa gun umman bashir kuma bata xuwa gunki. umma tace nida umman bashir duk daya ne intaxo gunta tamkan taxo guna ne. sai kuma habaicin da take jiyowa ta katanga sahura nayi.har ya kai umman abba na ganewa in bishira taxo, domin inxata tafi xakaji umman bashir tana cewa,to na gode yar albarka bakya gajiya da abin arxiki,ai ko baki kawo min komai ba yancina da kika fara qwato min kin biya ni. kuma ina tabba tan maki inkinga abba bai aureki ba baya ry/
ZURFIN CIKI book 1 part 4
ZURFIN CIKI book 1 part 4
Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 21:45
Wannan furucin ke sa bishira na qara shige ma sahura, duk wannan sha'anin da sukeyi abba bai sani ba. wanci tashi abba ya samu digree, sannan yaje kamp din shi a damaturu jihar yobe.sati biyu yayi sannan ya dawo. cikin sati biyun nan da baya nan ummi ta baxa iya shegenta son ran ta, umma ta qosa abba ya dawo saboda yanxune ta gane tsoran abba yake sa ummi tayi mata aiki da aike.dan tasan in ya sani baruwan shi da pushin tsohuwa,xai nakadetane, amma ahj da umma duk abinda ummi tayi daxaran xasu hukunta ta xata sa masu kuka tace dan de aci mata xarafine.shi yasa suka sakama ummi sunanta,sannan kuma suke dukanta a gabanta,imba hakaba maisa basuyima mai sunnan malan ba?dan dole suke qyaleta ,duk da ummi ta soma tasawa amma sam bata yi hankali ba. shekarun ummi sha uku tana js2 amma ko yaushe qara tirewa ummi keyi. addua kurun sukasa agaba,kuma sunsan allah xai amsa masu. Ranan da abba xai dawo ummi ta kama yima umma aiki da aike, dan kar a fadama abba. a ranan ne ummi taga wata alama da ta tsoratata cikin fitsarinta. a rudenta da hauka ta nufi gun umma tana cewa, umma na shiga uku

na, fitsarin jini nake yi. umma tace, wane irin kuma fitsarin jini? ummi sai tsalle take tana fadin ta bani ta lalace. umma tace ke xonan. ta jawo ta xuwa cikin daki, tace ke yimin bayanin yadda kika ga abin. ummi ta cire xani xata cire siket. umma tace, ke dakata min bance ki nuna min ba, yaya kalanshi yace? ko da tayima umma bayani sai ta fahince girmane ya kama ta. dan haka sai ta kamo ta ta xaunar kusa da ita, tayi mata bayani game da abin data gani, sannan ta nuna mata hadarukan da take ciki a halin yanxu. tace ummi ki natsu kiyi hankali, kisani yanxu kinkai wani matsayi wanda xakiyi taka tsantsa da rayuwanki. hadari na farko shine wasan banxa da maxa, kece mara hankali indai kin sama abokin wasa ba ruwanki da maxane ko mata ke dai kiyi wasa, Umma tace kisani yanxu xaki iya daukan ciki, indai har kika bari wani namiji ya shiga harkanki. ummi tayi xullo tace umma ciki irin na bara'atun baito? umma tace, eh ummi tace wanda har suka yar da yaran aka xo aka kama su yan sanda? umma tace tabbas. ummi cikin fargaba tace to ni umma baxan yi ba. ta soma kuka, to a kaini asibiti a bani magani mana. umma tace duk bayanin dana maki baki fahinta ba? ai wannan kin dunga yinsa kenan har qarshan rayuwanki, ko kuma in kinkai wani mataki na tsufa. ummi tace, to shi kenan, yanxu kuma inna yi wasa da maxa sai in xama irin na bara'atu? umma tace qwarai kuwa. ummi tayi tagumi tana tuna yadda suke tsokanan bara'atu inta fito. suna cewa tayi cikin shege tayi cikin shege! ta dubi umma tace xan daina ma yan maxa magana. umma tace ki dinga maganarki da kowa, kidai kula da kanki, sannan duk sokanan da kikayi da xunubin da ki ka kwasa to fa ki sani an bude maki fayel. Umma tace xunubinki xaki samu,gashi bakya san sallar kan lkc, sannan ga karya axumi.ummi ta sake tsurewa ,tare da fadin, to ba tsohuwa tace min inna mutu baxa ayi min hisabi ba,wai ni yarinya ce wai makarantan annabi ibrahim xa a kaini.umma tace da kenan kafin ki soma kalar wannan fitsarin, yanxun kam

in kin mutn xa a tambaye ki a cikin kabari, tambayoyi uku masu sauqi, masu wuya agun mara rabo.sannan xa a maki hisabi inkinyi mai kyau kiga mai kyau. tayi tagumi, umma ta manna mata tsumma a jikin pant. tace tashi kisa in kuma kinje gun haukan guje guje ya fado mutane sun gani shi kenan asirin ki ya tonu, kowa yasan kin girma. ummi dai ranan lafewa tayi kan kujera tanata tunani. tana kwance lkcn da ake hayaniyan dawowan abba kannanshi ne suka shigo mai da kayansa. qasa ya xauna a dakin umma, ya miqe qafa domin duk a gajiye yake. umma tayi ta dire mai abubuwan ci wanda tasan yanaso a gaban shi. sannan ta ba fati kudi ta sayo mai lemun kwalba, dariya yayi ya ce,ni dan gatane, shiyasa ina can ina tunaninki ummana, har nace inama ana tafiya da uwa da na tafi da ke.umma cikin jin dadi tace allah sarki abba, niko ina nan ina maka addua allaih ya baka abin da kaje nema,yace ummana kenan. ummi dai tana jinsu sam baima gantaba, sai can ya lura yace a,a kekuma lfy? umma tace bata dan jin dadine. yace tabdi,lallai kuwa ciwan nan yayi tsanani, ummi da ko a gadan asibiti take bata daina halinta? umma tace ai yanxuma nasan lafawa yayi ko ummi na? ummi dai kallansu take yi. abba yace allah ya yaye. suka ci gaba da firan su yana bata lbrn camp tare da nuna mata hotunan da suka dauka. yace dan ba kusa bane da kunje min kunyi kallo. ummi da xata bayi sai tafiya take wani iri tare da ware qafa. saboda rashin sabo. tsohuwa tace a,a takwara lfy? ummi tace, fitsarin jinin nake yi. umma ta fito da sauri tace ke ummi xo. tsohuwa ta saka salati, tare da cewa yarinnan nan badai faduwa kikayi ba. ummi tace nifa ban fadi ba hakanan ya xo min. umma tayi mata daquwa tace bayin kenan? tsohuwa tace ke suwaiba yarinyan nan faduwa tayi? da yake umma ta fahinci hausanta sai tace um,lkcn tane yaxo. tsohuwa ta saka salati tace, ni habiba yau naga abinda ya isheni? yarinyan yar shekaru nawane kwata kwata. lalle xamani, to sai ayi axaman aurad da ita. umma tace waxai kula ummi da

sunan aure ni suwaiba? ki kalla haukan data keyi a gari. abba cikin daki yace umma wa tsohuwa take cema ayima aure? umma tace ummi itama cikin dariya. yace tabdi jam to wannan takwaran taki waxai kwasa, ga muni ga rashin hankali.daga bayi ummi tanata murguda mai baki tana cewa eh din. Tsohuwa kuwa masifa ta hau yi,"gaka nan mara mutunci a gabana kake zagin takwara?kai mai sunan malam ka kiyaye ni" shi dai ya fita ya nufi dakinsa don kintsawa,yana mamakin ummi ta zama babba. Koda umma bata fada mishi ba ya gane haka ne ta yadda tsohuwa tayi maganar. tsohuwa ta dubi umma ta ce,"ki na daure ma mai sunan malam gindi yana ci ma takwara kashi a hannu,alhalin yana zaune a inuwarta.nan fa gidan ubanta ne." umma ta bata rai matuka,ta ce "tsohuwa ni da Abba da ummi duk daya suke a gurina,don Allah kada ki kuma furta haka har Abba yaji. kai ni da za a ce in zaba tsakanin ummi da Abba,na rantse Abba zan dauka."bata jira abinda tsohuwa zata ce ba,tayi ciki abinta. tsohuwa ta gama yan mitocinta ta shiga daki. Kwana biu kamar gaske,ummi an nutsu, amma abinda ya takura mata na daukewa sai umminku ta ci gaba da gashi, sai ma abinda ya karu. Abba ya daga ido sama yana kallon wasu tsuntsaye suna ta shawagi a sama, zuciyar shi tana cikin matukar damuwa sakamakon sheshshekan kukan da bishira keyi, bata san cewa ya fita damuwa da tafiyarshi kaduna ba? in ma da don ta ita ne da sauki tunda gidansu da waya zai iya zuwa (telephone) na bakin titi ya kirata. damuwar shi umman shi. ta katse shi "yanxu Abba haka zan daina ganinka?" ya sake tausasa murya."haba bishira, ina kano ina garin kaduna?" ta ce, "tabdi, nifa dalilin kukana taron matan kaduna nake ji, an ce kwarjini garesu. kawai kaje ka sa samu wata ka manta da batuna." Yayi murmushi "bishira kenan, kada ki dauka son da nake miki mai rauni ne da har zan canza wata dake, ni dai ki min addu'a." ta ce,"sam ban yarda da wannan zancen ba, ni dai bari in kira antina mijinta zai iya taimaka maka a barka kano." kafin ya ce komai

tayi ciki da gudu. yayi yar dariya. bishira tunda ya ce kaduna aka tura shi duk ta damu. Anti ta fito daga kicin, bishira ta ce, anti kizo inji Abba. anti ta dubeta, "in zo?" bishira ta kama hannunta "don Allah aunty taimako zaki mana, zo ki ji." 49- suka xauna sannan abba ya gaidaa anti cikin girmamawa.bishira ta dube shi ka fada mata.abba yace me?tace anti kinga fa kaduna aka tura shi,ni kuma wlh ba xan so yaje garin nan ba.anty ta sa dariya.to yanxu so kike yaqi xuwa ko so kike ya tafi dake? tace,ni so nake ki yima abban nasir bayani,nasan ba xai rasa sanin wani da ya sani ba.abba da anty suka sa dariya,yace kamar yaya?tace yayi magana a barshi anan suka sake tuntsira dariya.tayi fushi ta miqe fuuu ta nufi cikin falon gidan.anty tace bishira tana matuqan sanka,dan allah ka kula da ita.ya kalleta ya sunkuyad dakai,yace nima anti ina santa,kuma tuni nasa manya susan xancan,saboda in samu natsuwa,amma tace tana jin tsoron mamanta.anty tace eh to,dole taji tsoro dan ba dole bane hjynmu ta yarda,amma shi babanmu bashi da matsala.abba yace to ni dai xan tura a kowane lkc,dan ahjna yayi min magana tun kafin tafi ta camp. Din nan yake ta min zancan." Aunty ta ce,"to in kun tashi fa ba gurinshi za'a tura ba,gurin kaninshi ne dake jakara.amma kafin hakan sai an nemi izinin Alhajinmu din." Abba ya ce,"to ni ko wa zai shige min gaba gurin neman izinin?"aunty ta ce,"Abban nasir zan sanar dashi,insha Allahu har wannan din ma batun (service)din naka zan mishi bayani." cikin murna abba ya ce,"to na gode,Allah ya saka da alkairi"anty ta ce,"ba komai" ta mike "bari in turo ta don nasan tana can tana cika sai ka bata baki." yayi yar dariya tare da cewa"to". ta zauna tana kumbure-kumbureya ce"haba tawan har yanxu baki huce ba?" ta sake kauda kai gefe,ya ce"to shi kenan,yanzun dai na fasa barin kaduna." ta dube shi da sauri,"ka fasa barin kaduna fa ka ce?" yayi yar dariya"au na manta.kece duk kin ruda ni,cewa zanyi na fasa barin kano." ta share yar kwallarta,"to shikenan"

ya ce,"naji dadin kiran anty da ki ka yi.ina ganin nan da yan kwanaki su Alhajinku zasu sanni,Allah yasa ace an bani ke." Wayyo dadi,ta tuntsure da dariya.abbana nawa,bana zaton cewa zaka kai ni murna a ranar."ya mike zan tafi "ta ce tun yanzun? to ka ce ina gaishe dasu umma." Ya ce,"umma bata cin mike,kullum sai ta ci in gaishe ki da kyau.amma ke kin ki zuwa gaida ta." ta ce,"kasan fa ni bana iya sakewa da ita,nafi sakewa gurin umman bashir." ya ce,"kunyarta ki ke ji?" ta dan tabe baki tare da daga kafada kila. ya ce,"ina mamakin yanda kika saba da umman bashir,alhalin ummana tafi saukin kai." ta ce,"ga wannan kanwar taka mara kunya." ya yi yar dariya sabida tuno abind ummi ta musu. ya ce a hankali,"zaki saba da halin ummi."ta dube shi,"tun ranar dana soma ganin ummi din nan fa ban taba jin cewa ina sonta ba." ranshi yadan sosu,har ma ya gimtse fuska,amma baice kala ba.lura tayi da canzawarsa.don haka sai ta ce"ka min afuwa in na bata maka." nan ma bai amsata ba.illa sai da safe. Tamkar Alhaji yasan yadda abba suka yi da antin bishira,da safe Abba yaje gaida shi ya ce,"babana zuwa yanzun ya kamata a ce mun shiga maganarku da yarinyar nan." Abba ya sunkuyar da kai tare da ce wa,"um,dama gidan antinta da naje dazu munyi zancen,yanzun dai su ce sai an nemi izinin shi baban nasu. ta ce,mijinta zai masa magana,in yaso sai kuji ranar da zaku je din." Alhaji ya ce,"to shikenan.Allah ya kai mu.yanzu yaushe zaka tafi kaduna?" kafin abba ya bashi amsa,ya ci gaba da cewa,ban so ba sam da wannan yin nisan da zaka yi damu Abba." Abba ya ce,"ina hasashen cewa za a barni nan kano da yardar Allah,bisa ga taimakon mijin yayar yarinyar da nake zuwa gurinta." Alhaji ya ce,"to Allah ya yarda,sannan in an fada maka lokacin da zamu gana da waliyyan nata sai ka sanar dani." Abba ya ce,"to." Alhaji ya ce,"ina son mu danyi bincike kan yarinyar amma mahaifinta sannanne ne,anata yabonshi." Abba ya ce,"to." Ranar juma'a da misalin karfe biyu da rabi Alhaji ibrahim (wato abban nasir,mijin anty farida),ya

samu sirikinsa a gida. bayan sun gaisa ya tambayi yan jikokinshi sai Alhaji ibrahim ya ce,"suna lafiya.dama makasudin zuwan shi ne,akwai wani yaro da ke zuwa gurin bishira,yawancinan gidanmu suke zance. to gaskiya na yaba da hankalin yaron,sannan ya damu yana son ya turo iyayensa.to shi ne nace bari in nemar musu izini tukun." mahaifin bishira ya kalli surukinsa ya ce,"aisha ko bishira?" Abban nasir ya ce,bishira ce." ya gyara zama. "bishira ta gama sakandare ne?" Abban nasir ya ce,"ai Alhaji ba yana nufin ayi auren yanzun bane,a san dashi ne." Alhaji ya ce,"bana haka,ka sani sai dai tayi abu daya,in karatun karatun,in auren to auran. Ibrahim kasan wani abu daya? duk lokacin da kasa yarinya ta soma tsayawa da saurayi bayan tana karatu,musammanirin bishira irin wadda tasan tsarina amma ta danne ta turo min saurayi to gara ayi mata auren. Domin doguwan soyaryannan bata da ma'ana,qarshe sai wata shedana ta biyo baya,balantana bishira tana da rawan kai.ya matsa kusa da wayan tangaraho wadda aka jona ta ke amfani a daukacin gidan,ya dannan nanbobin sannan ya kira hjy.ta amsa daga sashanta,yace bishira na ciki? tace tananan, yace ki turo mani ita,tace to.gaban bishira ya badi,ganin mijin yarta a gidan dan tasan abinda ya kawo shi.ta xauna can gefe tace,gani dady,ta gaisa da abban nasir.mahaifinta yace nasan kinsan dalilin xuwan ibrahim ko? kanta a qasa tace,a'a. yace.yace to saurayin da ce xuwa gunki ne yake san ya turo magabatansa,kuma nasan kinsan da batun?sai dai inasan kisan abu daya bana san doguwan soyayya,da xara nagama buncike akan yaran wanda shari'a tace.inna gamsu,to fa aurad dake xanyi kije can ki qarasa karatun in kina so.ahj ibrahin yace yaran yace shi ba dole sai anyi yanxu ba.nufin shi a amince mashi.shi kuma xai jira har ta gama makarantanta. ahj ya katseshi ta hanyan daga mai hannu,ibrahin kaidai sheda ne bewan bana haka, kuma ba a haka dani ko?yace auran yata fa kakeyi,ka san tsarina.ibrahinyace na sani ahj.

yace yauwa,ina nan ban canxa ba.yace yanxu abinda nake san ka dashi kafin na amince da xuwan iyayan shi.ya dubu bishira yace kinasan shi kin amince dashi? tace eh yace tashi ki tafi angama.kai kuma inasan kashiga unguwa uku ka binci komin labarin yaran da usilin shi.ahj ibrahin yace angama.yace naso ace sai ta gana karatu,dan sai anyi sa'a xata qarasa,anma hakan xaifimin akan doguwan soyayya kafin inxo inajin haushi.ibrahin ya miqe to ni xan tafi.ahj shima ya yunqura xai tashi sai waya ta kama ruri dan haka sukayi sallama anan. ummi ta shiga gida daga makaranta take,akuyan umman bashir tagani ta gani a gidansu tana masu barna a kicin da sauri ta koma ta saka sakatan gidan,sannan ta dawo.ta kama akuyan ta kaita bakin fanfo ta tara kanta sai kuka akuyan take tayi. Umman bashir ta jiyo daga gidanta,da sauri ta fita taxo tana buga gidan tana mashifa.yan baqin ciki,mahassada,yanka min akuyan xaku yi?san ummi bata ji ba, dan gidan ba kowa. umma taje sheka can gidansu,hta kuma tsohuwa taje gaisuwa n mutuwa nan kusa dasu.saida taga akuyan ta galabaita sannan ta janyo wata leda ta daura mata a bindi,sannan ta saketa.akuyan ta tashi da gudu tayi hanyan fita,tace shegiya gobe kixo ki bude mana abinci kici.taje ta bude qofar ta jiyo muryan umman bashir,dan haka sai ta cire sakatar sannan ta dan sanmata qofan akuya tayi waje da gudu.saboda ledar da ummi ta qulla mata,sai take ganin kamar binta ake,dan haka ta nausa cikin unguwa da gudu.umman bashir na ganin akuyarta tayi fitan bindiga,sai tabi tana cewa,ku taremin.ummi ta koma ciki tana dariya.ita kuma umman bashir daqar ta samu aka ruqo mata akuyan ta.aka kwance ledan taruqo ta xuwa gida.sai masifa take, tana isowa qofar gidan umma na RFIN CIKI book 1 part 5

ZURFIN CIKI book 1 part 5

Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 21:54

Ita kuma umman bashir daqar ta samu aka ruqo mata akuyan ta.aka kwance ledan taruqo ta xuwa gida.sai masifa take, tana isowa qofar gidan

umma na isa. tace yar baqin ciki kun kama min akuya kun jiqata xaku kashe min,ta ta allah ba takuba.umma tace akuya kuma wani iri?ni bana gidan dawowa ta kenan.ta ce kina nan muna fuka.umma sai ta shige gida,amma duk da haka sai da umman bashir ta bita har ciki tace sai ta doke mace akan akuyan ta.umma ta shige daki can qurya tasamu ummi a kwance,tace ke uwar yan daukan magana, ke ce kika jiqa mata akuya? umma tace cinye min abinci tayi.nan abba ya riske ta tana ta tsine tsine.yace meya faru?tace kai ja can ka bani guri,dan baka san darajata ba,banda an raina ni yaya xa'a kama min dabba a jiqa?in nai magana sai a maidani mahaukaciya ko haquri baxa a ban ba.abba yace to kiyi haquri in sha allah baxa a qara ba.tace baxan haqura ba,tunda inta mutu nike da asara.umma tafito tace to yanxu ya kike san ayi?ni dai bananan ummi ce da wannan tsiyan wai ta sameta ta cinye mata abinci. umma tace kinsan halin ummi kuma nima haquri nake da ita.tace to ni baxan iya haqurin ba.umma ta finciko ummi ta hanka da mata.ta gata na ki rama mata.ta juya cikin daki ta kama harko kinta.ba kunya ta kama ummi tana ta jibga.abba takaicin mahaifiyan shi ya cika mai xuciya,amma bashi da daman cewa ta bari.shin baxa tai tunani ba takama yar matan da tariqe mata danta riqon adalci da amana,tana duka haka? sai data gaji dan kan ta sannan ta fito.abba ma fita yayi cikin takaici,ummi kuwa kuwa tayi tayi har tsohuwa ta dawo,ta sameta xaune tana dirxan kuka. Dama taci karo da abba a waje tace mai sunan mlm har ka dawo xaka kuma fita?yace um.tace miskilin banxa saikace mai ciwon hakori,ta riska ummi tana kuka,tace umhum daman tunda naga ya fita yana ta maxurai nasan yaci xalinci.kai na gaji da halin mai sunan mlm.umma tace,ba ruwanshi.ummi taqara satin kuka ba umman bashir bace taxo tayi min duka.meki ka mata?wai din akuyan ta taxo ta cinyemin abinci,shine na jiqata da ruwa,shine taxo tamin duka kuma gashi banci komai ba, ko qala bata ceba,ta juya sai gidan

umman bashir.ta sameta tana sinke kayan miya.tace ke sahura saboda bakida mutunci shine xakixo har gaban uwarta ki daka?sahura tace na daketa,kamme xata jiqa min akuya?tace wane shegen ne yace ki saki akuyan ki har taje taci mata abinci?to kashedin ki mara mutunci da baki san girman nagaba ba.bashir ya fito yace a'a tsohuwa kidaina xagan mana uwa har cikin gidanmu.tace iye!kaxone ka nuna min rashin tarbinyan ka?nan har wata uwa gareka?nanfa sa in sa ya tsarke a tsakaninsu.ummata juyo su tarasa yadda xatayi,sai ga abba ya shigo.yauwa abba shiga gidan can ka lallaso min tsohuwa taje kasgedi ataba yar gwal dinta.ta dubi ummi tace duk aka yar marajin can ni naji dadin dukan da tayi mata,dan dukan algaki tayi.banda xalunci ya xata kama dabba ta jiqa? abba ya fita ba tare da yace qala ba. abba na shiga gidan bashir yana tsigale tsohuwa tankar xai kai mata duka,abba ya daga hannu ya wanka ma bashir mari,sannan yace tsohuwa saankace da xaka dunga mata wannan fadan.ya dubi umman bashir dan allah kiyi haquri.sannan yaja hannu tsohuwa,shi kuma bashir yana ta xagin abba yana cewa allah ya isa. umman bashir ta ce abba tir da hauhuwan ka tir!tir! kuma gab nake da in dagama ka nono.cak! abba ya tsaya kalaman mahaifiyan shi sun shi jeshi,a hankali ya saki hannun tsohuwa batare da tasan ya tsaya ba.dan sababin da takeyi yaja hankalinta.ya juyo har gabanta yace dan allah ki yafemin ki ya femin.ba tareda ya jira amsan ta ba ya fita. baiji muryan taba amma koda bata ya fe maiba jikinta yayi sanyi.da yamma bayan su ahj babba sun dawo kasuwa sai suka shiga dan gaida tsohuwa.nan ta saka masu kuka suka rude tare da fadin me aka mata?cikin kuka tace ni sahura xatai ma rashin mutun ci tare da danta bashir nan ta koro masu bayanin komai. Ahaji dai sukai ta bata haquri,ahj qarami yace shi kam dole ya cimata mutunci daga ita har bashir din.da suka fito ahji babba ya ce kada gaje ka mata da tsin hankali,nashihaxaka yi mata shi kuma bashir ya girmama yayansa.abba kuwa yana fita sai ya

bar layin dan bacinrai,dakin ahmad yaje ya kwanta duk da cewan ahmad din bayanan.tunani yake tayi akan mahaifiyanshi,yadda ta runtse ido da alkairin da umma da ahj suke mata.ahj qarami cikin damuwa da takaici ya shiga gidansa,da bashir ya soma yin karo,nan take ya rufeshi da fada.sahura na ji ta taso cikin mashifa kada ya xagan mata da,dan ya nemi tare mata mutunci.ahj yace har wani mutunci ne dake wanda xai kare maki?to da kinada mutuncin kin tunkari mahaifiyata ki mata cin xarafi?tace har gidannan ta shigo saboda na daki yar gwal dinta,takan wannan wara mutuncin yarinyan xata xo ta xage ni?umma tace ma ahj babba ka fito gashi can fa ahj qarami rigima ta kaure tsakaninshi da umman bashir.da qyar ahj babba ya kashe wutan,abba da ya dawo yaji hayani ma mahaifanshi sai ya qara barin layin sai can sha daya na dare ya dawo ya kwanta,ranan ko abinci bai ci ba.da safe yana gaban umman shi yana fada mata kalaman da umman bashir ta masa jiya,una ta ce ashsha,kai banji dadin wannan kalaman na sahusa gare ka ba.saidai na gode daka nemi yafiyanta,sannan ka kiyaye duk abinda xaisa tayi maka munmunan furuci.dan bakinta dafine a gareka.kada kaga cewan baka yimata komai ba,to intayi ma mugun furuci sai kamaka.yace xan kula,tace yauwa abba.saka makon binci ke da mahaifin bishira yasa amishi iri daya da wanda sirikinshi ibrahim yayi mishi,ma'ana halayan kirki da mutuncin iyayanshi da shi kanshi yaran.duk dadai ance masa ba wasu masu hali bane?sai rufin asiri da suke da shi.wannan bai dameshi ba tunda dai ance mashi yaran yana neman na kanshi,sannan yana karatu. to tunda tana sanshi ba ruwan shi. ya kira wayan cikin gida ya kira hjy sai yaji sallamanta ta turo qofa.yace yauwa dama ke xan kira.ta dire tire mai dauke da kayan shayi akai,sannan ta xauna tana gaishe shi. Ya amsa sannan yace ina jin gobe masu neman auran bishira zasu je wajen yaya a jakara. Hajiya zainu ta gyara zama,"ka ce, bishira ko Aisha? ya ce bishira dai tayi yar dariya

yaushe bishira tayi saurayin da har zai turo? ya ce,"a'a ba ki sani ba? ta ce,"na dai ji yanzun" ya ce to na basu izinin turawa tun jiya tunda tana sonshi babu ruwana da doguwar soyayyar nan kin sani Hajiya zainu ta hade rai,"amma kana sane da cewa ss2 zata je ko? ina laifin ta gama sakandare? Tace ,"gaskiya ranka ya dade ka bar batun auran bishira." ya dubeta,"kada ki damu kanki fa.don kin san ba zan canza ba" ta bata rai,to dan wanene? shima ya daure fuska dan babanshine.ta mike a fusace ta fita sai dakin su bishira. Lokacin suka farka daga baccin da suka koma bayan sallar asubahi.ta ce,"ke bishira,ke ce kika turo saurayinki gurin dadynku? wai yaushe ma kika yi saurayin? Aisha tayi zaraf tace, momy kin ma san wanene? hajiya zainu ta ce,"wanene?" Aisha ta ce telanmu Abba din nan." Hajiya zainu ta saka salati Abba tela? tela fa? Aisha ta ce,"tela kuwa" hajiya zainu ta isa gurin bishira ta rike mata kunne. "kece kika zabi auran tela? me ya ci shi kansa bare ya baki? zai iya da karatunki? wallahi tun wuri kije ki fada ma dadynku bakya sonshi." Bishira ta ce,"nifa shi nake so momy."hajiya zainu ta rufeta da duka. washe gari su Alhaji babba da abokinsa Alhaji sani,sai makocinsu malam ma'aru suka je nemawa Abba auran bishira a jakara gidan Alhaji musa wan mahaifin bishira. an amshesu hannu biyu,sunyi magana ta fahimta an basu,kuma sun karba.an yanka sadaki da dukiyar aure,sannan sunce suna so za'a hada da yarta. Su Alhaji suna ta godiya nan dai gemu da gemu suka rabu cikin mutumta juna. Hajiya zainu ta dauki karan tsana ta dora ma bishira,tunda tayi-tayi cewa ta janye batun auran Abba taki,ta ce to bazan miki komai ba.sannan in babu ta sameki kada ki ce kin sanni,in ki ka zo nan gidan da sunan neman taimako saina wulakanta ki. Duk bishira dai ta yarda,nan aka sa rana kusan wata shida. Abba ya iso kofar shagonsu da sauri don hangen da yayi gurin ya cika da jama'a,yana zuwa sai yaga ashe ummi ce tazo wucewa ta taba wani shagon fale-fale ta taba sai yayi mata shocking. shikenan

ta tsaya tana jiran wa zai zo tasa shima ya taba,can sai ga wani yaro,tace kai ka iya karatu? yaron ya ce,"eh" ta ce karya kake in da gaske ne nuna mun acan.da gudu yaro yaje ya dangwala dan yatsa a kan A sai ko shocking ya debe shi ya jefa kwata. Ashe yayan yaron na kallonta sai ko ya biyota shine ta fallo da gudu ta fada shagon,shi kuma y ce sai ya duketa. Abba ya kalleta kallon tsana ya ce,"fito shegiya ya hankado ma yaron ita ya ce ka mata dukan tsiya yaron ya ce na hakura ta ci darajarka Abba ya ce don Allah ka duketa,don wannan bata da wani amfani daya wuce duka. yaron ya ce,ku dai ku ja mata kunne don kar taje tasa dan wani a matsala,ko ma ya rasa ransa,domin shocking zai yi kisa nan da nan. Abba ya ce dama zai kasheta ai da munyi murna.ummi ta kalleshi a ranta ta ce sai kazo ka kashe ni. Bayan kowa ya watse na nan yasata tsalle kwado. Ahmad abokin shi ya shigo shagon ya ganta tana ta tsallen kwado ya ce a'a Abba meye naka nasa mace irin wannan horon? Abba ya ce kasan Allah da ace yarinyar nan namiji ce da tuni na zuga an kaita gidan horon yara,kaini da in kayi kisan kai babu laifi da sai na ba yarinyar nan gamalan 20 tasha ta mutu. Ummi cikin kasa-kasa da murya ta ce nima da zaka mutu a dadina. Ahmad ya ce haba Abba ya kake irin wannan maganar? ya dubi ummi tashi ki tafi abinki.ummi taki tashi don tasan in don Abba ne sai ta tashi ya ce ta sake sabon lale don haka sai ta ci gaba da tsallan kwadonta. kuma bata nuna kasalarta domin ya ce sai taji jiki tukunna zai barta. wannan ya shigo ya ce Allah sarki ai mata hakuri wannan ya shigo ya ce don Allah a kyaleta.sai kurum ta saka kuka. da kyar Ahmad ya shawo kansa har ya ce ta tashi ta tafi.ya ce kuma inta yarda yazo gida ya samu tayi wani laifim shi da ita ne.daf da magrib yana sauri za shi masallaci sai ya ganta da dan tasi tana kasa shi kuma yana tuko motar a hankali yana ce mata an kusa gidan tana cewa eh. bata lura da Abba ba saida ya ce ke ina zaki? da sauri ta fice da gudu dan tasi yace ke yarinya zo nan.

Abba ya matsa gurin shi ya ce malam lafiya? dan tasi ya ce yarinyar can ce ta taro ni tun daga bakin titi.wai an aikota ta kira dan tasi za'a dauki kaya zuwa wambai. nan na dibo fasinjan cikin gari ne ma sauke su tare da basu hakuri,to da mukazo hanya sai tace mun jaki ne za'a dauka nace jakin lafiya? ya ya za'a iya saka jaki a tasi? ta ce mun ita dai tashi aka ce mata ta taro,kuma nayi-nayi ta shigo motar taki. Abba ya ce,kayi hakuri karya takeyi,kanwata ce.wallahi bata ji. dan tasi cikin takaici gashi ya sauke fasinjanshi yajuya ya tafI. Abba ya nufi masallaci yana kyalkyata dariya.don shi lamarin ummi tsoro ma ya soma bashi jaki a tasi.kai shima dan tasin mashiririce ne.banda haka tunda ta furta jaki ai sai ya kama gabansa. yau bai ma bi ta kanta ba.don yana sauri yaje gurin masoyiyar sa bishira. Ummi ta shiga ajinsu na makaranta.kai tsaye ta nufi kujerarta wadda babu wata yarinyar data isa ta zauna duk ajin don suna matukar tsoron ummi. Tun daga lokacin data bigi kirji ta ce kujerarta ce,kowa ya sallama mata.malamai ma da suka gaji da rabon fada cewa suka yi a bar mata kujerar. duk makarantar babu wanda bai san ummi ba,malamai da dalibai saboda yawan fadanta da tsokana,har malamai bata bari ba a tsokana. sun fita fitsari ita da kawarta Amina,kafin su dawo malamin (social studies)ya shigo. Amina ta ce ummi dubi har malamin(social studies)din ya shigo. ummi ta ce,"ina ruwana,ko wanene ma ni shiga zanyi abuna."Amina ta ce,"in dai tica hassan ne gara mun juya don sai ya zane mu." ummi ta ce,"tab ai gara dukanshi da in tafi gida yanxun wannan mugun yaya Abban ya ci zalina." sam ummi bata kalli malamin ba,sanda take takai kujerarta,yayinda Amina ta labe ta kasa shigowa,kamar cikin mafarki taji muryarshi y ce,"ke daga ina ki ke?" ta dubi gurin da sauri,"yaya Abba ne ya hade rai,fuskar nan tashi babu annuri sai kace mai bada mugun labari. ta tsorata matuka,ya ce" zo nan kiyi 'kneel down'." jiki na bari ummi taje ta zube gaban allon.nan take yayi mata bulala guda goma masu kyau.

take yan ajin suka shiga taitayinsu,don sunga ummi tsiga tana kuka irin wanda bata taba yinsa ba.don ko an duketa daurewa takeyi ta kuma shanye dukan. sannan sabon malami dan bautar kasa kamar yadda ya gabatar musu da Kansa daga zuwa yayi wannan duka.lalle dole su tsorata. ya ce,wuce ki zauna dakikiya mai idon jaki.wannan kalma ta daga hankalin ummi,domin taga yan ajin sun guntse dariya. ummi ta koma kamar ruwa ya cinyeta a cikin ajin duk tsokanarta ta tsiya,tsunguli wancan,shuri wancan,duk an samu saukinta. taimako daya Allah yayi mata,duk da halinta ta da kan daukar karatu.a zaton Abba bata iya komai ba,tun da basa shiri. don haka baya ko duba takardunta,islamiya ne yafi tsarata don tashi hikimar fannin addininta ne dole a matsa mata ta sani,boko kuma in bata yi ba ta yiwa kanta. duk rubutun da Abba yayi ummi yake ta dawowa ya ce ta karanta shi in ko ta mike sai ta karanta shi tsaf.in da ta dan samu saukin shi kenan. tun daga wannan ranar ummi alkadarinta ya soma karyewa gurin yan ajin,domin in suna fada shh da yazo ba bin ba'asi ita yake horawa. sannan in ta duki wani kafin ya shigo.daya shigo za'a fada mishi,don shine ya basu damar cewa duk wanda ta taba in yazo a fada mishi. duk da sun gano kanwar shi ce,gashi kuma wani lokaci tsokanarta suke tunda ya ce mata ummi mai idon jaki. sam bataji dadin zuwan Abba ba amma tasha alwashin itama sai ta mishi abinda zaiji bakin ciki kwatankwacin yadda taji. wata rana Abba ya siyo wayar sadarwa, lokacin tana farkon fitowa,yazo da ita gidan yana nuna ma su umma. nan akayi ta mishi murna umma ta ce,"kai Abba,kai da zancen aurenka ke karatowa ina kai ina siyan wannan abar har kusan dubu ashirin ka ce?" Yace umma amfani kai,kema xan sai miki ai tunda nan gaba kadan xata sakko.ahj babba dai yace xaya bani kudi in sayo musu shida ahj qarami.ummi na wanke wanke tana kallan su,wayar ta birgeta,irin wanda suke gani a cikin fina finan indiya, ta xata yan sanda ne kawai suke riqe irin wannan wayoyin.kai ko na bakin

titin nan da take ganin mutane na bugawa birgeta yake yi,har ta tuna ranan da sukayi doguwan tafiya sukaje phone book.suna xuwa suka tarad ana layi,haka suka koma gyefe saida kowa ya gama sannan suka shiga sunata latsa latsan nanbobi suna karawa a kunne.saida wani mutun yaxo ya kore su,bayan ya dundungure masu kai. tayi murmushi, sannantace a ranta, allah yasa ya sai ma umman su,ita ko ta samu abin latsawa. daya nunama tsohuwa wayan tace shirman banxa,inba qarya ba da wannan xaka kira wani daga nesa?yace kn da a saudiyya kike xan kira ki.ta ja tsaki tayi daki shiko ya fice nana dariya.cikin satin ahj babba ya ba abba ya hada masu waya da layi,ahj babba yafi kowa murna da wayan, saboda shi mata fiyine. Wata safiya abba ya shiga wanka, umma na kicin tana soya masu dankalin hausa. zirif ta shige dakin abba tanata danna danne,da taji motsin bayi sai ta aje ta yi waje da gudu.saida ta tabbata ya shiga daki sai tayi xirif da shige gida.lkc da taxo kawo mai abin kari tasame shi yanata danna wayan,ya dubeta kinxo kin tabamin waya ko?da sauri tace a,a.yace munafuka,kece gashi kinyi min delete din duk numbers din dake cikin wayan, muguwa. tace to ni na shigone?ya harare ta yace fita, da ace ban rubuta lambobin na aje ba da yanxun kin min asara, muguwa kawai. ummi ta fita tana dariyan mugunta,domin in da abin da tafi so bai wuce taga bacin ran abba ba,kamar yadda tayi imani shima burinsa kenan. umma ta lakato man xafi tana shafama ahj a qafa tana murxawa.yace yauwa suwaiba kamar kinsan tun daxu yakemin kwankwatsa.daxidariya tace in dan tamu ne kariqa ware ranaku biyu a sati kana hutawa.yayi yar dariya,ina wani hutu da xanyi a gidan nan,matsalar ummina kadai ta ishe ni.umma tayi dariya,sannan tace ai ummi sai addu;a Ta canya xancan da cewa,af na manta niko yanxu auran abba yayi wata hudu nangaba?ya ce hudu ne da yan kwanaki.tace tofa!gashi ni uwarsa banida ko kobo,bari naxo na kama sana'a. ya tuntsure da dariya,sannan yace sai yanxu kika san da

sana'a?itama dariyan tayi tace, in ba haka ba ahj ranar biki ko an kirani bana amsa ba.yace gashi kuma ke xaki mishi lefe.tace,to na shiga aljihunka,in yaso in an soma sana'a sai in biya ka.yasa hannu ya dago fuskanta yace sannu sarkin wayau.suka sa dariya.yace in san muje yaga gidajen nan na layin gabanmu,sai ya xaba guda daya a baiwa masu hayar notice sai a gyara shi.tace ya xabi na farkon layin dan yafi kxau.yace amma bashida girma.tace ya ishe shi daga shi sai matarsa fa?wanda ke cikin gidan ba mata bixu ne dashi ba?yace to xamuje dai ya xaba.sannan akoma kan lefe,tace allah ya saka da alkairi,allah ya kaimu.yace amin.wayanshi dake caji ta soma ruri,yace dauko min wayar can.ta miqe tana cewa har naji tsoro,na kasa sabawa da wayan nan.yace kuma gashi na kusa bar maki ita. tayi dariyan jin dadi,tana kallanshi.to ni wama xai dinga kirana?yace ni mana,bana iya yi miki wata magana in na kira abba na ce ya kawo maki,sai inga kamar yana tsaye,inko taki ce dana kira sai ki kebe daga jama'a muyi hiranmu. tayi dariya, daidai lkcn da kiran ya sake shigowa,ya daga. ahj buhari ne wanda ke sarin kaya gun shi daga kaduna.suka gaisa yace ahj ka kira kan in dauka ta katse.ahj buhari yace,dama ina san ince maka ne dan allah gobe xan shigo,kasa ahada min kayan nan da wuri.yace ba komai xa a hada.bayan sunyi sallama umma tace ni abin da yake bani al'ajabi da wayan nan, har kullum yanda xaka kira wani daga nisan duniya,kuma kuyi xance radau.ahj yace ci gaba kenan,wata rana ma sai kinga fasahan data ninka wannan.tace haka ne.abba yana xaune gaban ahj da safe bayan sun gaisai,sai ahj yace abba ina ganin da yamma ko xuwa dare kaje ka duba gidajen nan ka xabi guda,saboda a ba su notice dan a gyara didan.yace ahj ba sai naje ba duk wanda aka bani yayi.ahj yace ummanka tace ka xabi na farkon layin. cikin murmushi abba yace,ta shi kenan,nima shina xaba domin duk abinda umma ta xaba min shine xabina. tuni sahura ta fito da

anko,xaqewanta da nuna isarta akan bikin sai kace ba dan fari ba. duk dangi sai surutunta ake yi,har danginta.umma kan cewa tayi anko ba shine damuwanta ba,dan haka sam bata bi ta kansu ba.abba a cikin ajin da yake koyarwa,ummi tana 2n gefe in da yayi mata maxauni a qasa,can in da ba knwa sakamakon ganowa da yayi in tana ajin ba a xaman lafiya,sannan babu me ikon xama a kujeranta.yace,in ma ya sake ganinta ko a wace kujera ce bas,xai ballata.rubutunda yayi take yi ranta bace.ya kalli gun datake yace ke!ta dago ta dube shi,yace xo nan.taje yace,amso min bulala acan ajin.kafin ta dawo sai da ta duke wata yarinya ta rugo.nan kuwa yarinyan ta biyo ta har aji,abba kam daya amshi bulalar saida ya xaneta tas.sam abba ya sama uni ido ko ta ina,ba makaranta ba, ba gida ba.dan haka ta matsu yayi aure ya bar gidan sannan ya gama service dan shi ya qara gaba. tabbas lkcn auran sa xata yi party.RFIN CIKI book 1 part 6

ZURFIN CIKI book 1 part 6

Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 21:56

Tabbas lkcn auran sa xata yi party. Ummi party xatayi na murnan barin gidan shi.ahj ya ba umma wayarshi kamar yadda ya fada mata,ya ba abba ya suya mata layin mtn kamar yadda ya fada mata.ummi tafi kowa murna da wannan wayan,domin in umma ta aje takan dauka tayi ta latse latse,har dai ta iya abubuwa a wayan saboda ta iya karatu.kwanci tashi bikin abba ya rage saura yan kwanaki.duk gida biyun sai shirya shirye suke,mu samman gidan amare saboda yan mata biyu xasu auran.gidansu abba tuni ahj yasa an masu fantin gidan biyun,gidan ango kuwa ya sha gyara da fenti.ahj ya sabunta mishi qofofi da wundunan gidan, batun lefe kam dama tuni ya ke sayen xannuwanshi da kadan da kadan yana kawo ma umma tana adanawa.dan haka ahj karami yana kawo akwatuna umma ta fito da kayan dan tasan me xa a qaro.sannan ya yaba da hankalin abba.wannan ya nuna mishi cewa abba xai iya riqe gidanshi.lalle sana'an hannu tana da amfanh ga yayanmu a wannan xamanin

namu.umma tai mashi lissafin sauran abubuwan da xannuwa da leshi xuwa shadda,tace ahj dan allah adubo mana masu tsada, Ahj yace suwaiba xan yi daidai qarfina,ba xan yi qarya ba dan sun san cewa dana talaka ne,kuma suka ba shi.umma tace,sai batun abin da xa a ci.yace suwaiba kenan,saunawa xakimin lissafin kayan abincin?na xata ma xakice kayan sawanku?umma tace suma a kawo mana da wuri dan mu dhnka da wuri,ba abba xan ba c saboda harkokin sun masa yawa.saura sati uku biki aka kai lefe.hjy xainu dai unguwa ma ta tafi a ranar,danginta na maigidan su ne suka amsa.sai yatsina suke tare da raina kayan da suka duba ma sai um da um suke cewa,wata tace to an gode fa,tunda taji ta gani mu menene namu?suka ba da tukuici, nan dai yan kai lefe suka dawo jiki babu qarfi.koda suka dawo suka sanar da umma sai tace ku qyale su.mu dai mun yi daidai qarfinmu.umman bashir kuwa da qannanta suka kai mata labari cewa,tayi ina ko xa suyi maraba da kaya?suwaiba ta karbe mishi kudi bada xuba kayan kirki ba,banga laifinsu ba.ummi kam sai dibar ma umma kayan abinci take a boye tana kaiwa gidan maman iman maqotansu ne,matan suna shiri da ummi, don ita rayuwar ummi dariya take bata,ta gwado shinkafa ta kawo,taliya,ta tsiyayo mai,ta ce sauran kayan miya da magi,har nama debowa zanyi. maman imam ta ce lallai kawayenki zasu sha party. ummi ta ce tab ai dole inyi party zan rabu da alakakai sarkin mugancin duniya. maman imam ta saka dariya,ummi ta kuma fita da gudu tana fadina na tuna inda gishiri da maggi suke. daga gidan amare anzo anga gidan amarya,nan ma sun tafi suna mita,fadi suke "bishira batayi sa'ar miji ba,wata ta ce ya aureta ne don kudin ubanta. koda suka je suka fada ma hajiya zainu fasalin gidan,daki uku ne duka falle dai dai sai kicin da bayi a tsakar gida. kanwar zainu ta ce,"kai gaskiya bishira bata yi dabara ba.hashimu dan gidan Alhaji mansur ya jima da sanar dani ya kamun bishira." hajiya zainu ta ce,"shi kadai?ko yayan abokan babansu nawa ke sonta?tunda taki

tsayawa tayi karatu ta zabi ta auri tela,ba shi kenan ba?dubi gidan ubanta amma ta zabi zama a wani gida dakuna jere sai ka ce ajin primary."lol. suka ce,"kwarai kuwa kamar ajin makarantar gwamnati."ta ce,"shi kenan ai kaya dai asai mata daidai tsarin gidanta ba iri daya za a sai musu da Aisha ba." sun siyo sunje sun jera komai ras,yanzun kam sai daura aure ya rage,Abba da abokanansa walima kadai ya shirya. can gidan ne suke ta bukukuwansu irin ma masu hali.shi kam dai yasan yan'uwanta ba sonshi suke ba. sam be je gurin shagalinsu ba. ranar lahadi aka daura aure,misalin karfe goma na safe,unguwar kam ta cika da mutane da motoci. Abba da zugar abokananshi salisu yayan amare yayi musu jagora cikin gidan. sun gaisa da mutane sannan suka fito kowa fadi yake."kai amma angon bishira zankadede dashi tubarkalla."gashi Abba da iya daukar wanka,tsafta ce dashi ga son kamshi. KAI MATA IYAYEN GULMA. Can gidan ango ma anata shagalin cin abinci, jama'a dangi da makota sa gudunmawa suke ba umma tana a'a amma sai ace ta rike sabida ita mutum ce mai kyauta. umman bashir kam sai takaici take ji,kowa ya shigo sai dai ya ce mata."Allah ya sanya alkairi"kawai musamman ta shigo gidan don taga ko ana ba umman Abba ne. Nan fa na fita ta koma gida babu ko kunya tana ta masifa, fadi take "lallai suwaiba,gudunmawar auran dana duk ita ce ke karbewa? gaskiya naga sai dai amin Allah sanya alheri a wuce,to da sake,ni na haifi abuna ta bari sai ta tashi auran wannan figaggyar yar tata sannan ta amshi bikin." ta gama fadanta ta matsa,danginta suka soma yi da ita,suka ce wa zai baki wani abu ke da ko dan uwanki baki san ki bashi gudunmawa ba bare kyauta.tsinanni yar rowarki ce taja miki." kanwarta ta ce,"sahura sai dai ta ci na wani ba dai aci nata ba,dama irinsu sun cika son banza." ummi kam anci kwalliya an gayyato kawaye anata party a gidan maman iman,an kunna rediyo sai rawa suke yi,kafin a gama partyn an bige da

fada da dambe,da kyar aka rabasu,nan taro ya watse. da misalin karfe takwas na dare,ango da abokanshi sun taso sallar isha'i Ahmad ya ce don Allah ango muje mu rakaka. ya ce,"Allah sai nayi wanka."mukhtara ya ce,"gidan cunkus da jama'a zakayi wanka?" Aminu ya ce,"don Allah malam kazo mu tafi,in ma kifi zaka zama a gidanka." Abba ya ce,"bari dai ku gani." a zaure suka ci karo da ummi,ya ce,"ke jeki ki wanke bayi ki kai mun ruwan wanka." ta sobare baki ta koma ciki tana fadin. na dai kusan hutawa, masifaff. ta wanke bayin sannan takai ruwan,yana shiga gidan dangi sukayo kanshi,ga ango! ga ango!! abokan wasa suka za na can zamfara suna tayi masa tsiya. dan gidan ummanshi yau dai za a kwana wani gidan ba na umman tashi ba.ya dai samu ya shige wanka. bayan ya fito ya bude dakinshi,ya shirya cikin wata shadda mirror,lokacin su ake yayi.ruwan kasa mai duhu. yasha hula mu hadu a banki ita ma kalar shaddar,ya feshe jikinshi da kalolin turaruka.ya shigo cikin gidan yaje kofar dakin umma. ya ce umman tana nan.aka ce mishi tana dakin Alhaji,yayi sallama a kofar falon Alhajin basu ji ba,suna ta hira tsit ya yi lokacin da yaji umman tana cewa Allah dai ya basu zaman lafiya da zuri'a tagari. Amma har ga Allah naso Abba ya auri..... ringing din wayar shi ce ta hana jin kowa ummanshi ta ce,sai dai muryar Alhajin ya ce wallahi suwaiba nima tsarina kenan. ahj yace ta allah ya riga ya shirya ba ita ce matarshi ba.ya daga wayar,ahmad ina xuwa mana. ba tare da yaji abinda ahmad din xai fada ba ya katse kiran,dan yaji haushi.yaso jin wacece iyayansa suka so ya aura?ya sake doka sallama,suka amsa.ya shiga ya xauna ya gaishesu,sannanya dubi umma.dama naxo miki sai da safe ne.ahj da umma suka yi yar dariya,umma tace to abba,yanxu dai ka girma,dan allah kyawawan halayenka dinnan kaci gaba da su.yace na gode.ahj ma yayi masa nasiha,daga nan ya fita jikinshi a sanyaye.da muwarsa me yasa umma bata sanar da shi yarinyar da taso mishi ba

tuntuni?haka dai suka rankaya da abokanansa dan xuwa dakin amarya. gidan kam tun daga tsakar gida qamshi ke tashi.sun taradda qawayenta biyu,ita kam tana lullube kan gado.nan dai suka sayi baki akayi yan shaqiyanci tare da barkwanci,sannan qawaye suka yi mata sallama suka tafi,shima ya raka abokansa. ya dawo ya xauna bakin gadan yana dubanta, itama kallonshi take cike da so. sukayi ma juna murmushi,ya janyo ledan kaxan da suka shigo da ita. Ya warware takardar,y yago cinya ya mika mata a baki,"ci,nasan yau kin wuni da yunwa ko?" ta ce,"na koshi bana jin yunwa ma,ni kam duk yau banji yunwa ba." ya ce,"ni ma haka,dama yau bai da ce muci abinci ba."ta dube shi da alamar tambaya a kwayar idanunta.ya ware idanunshi. "taron da muka tara ko ina cike da jama'a." yayi yar dariya sannnan ta bude baki ya saka mata kazar.ta dan figa.haka yayi ta bata tare da zuba mata juice a kofi shima yana bata. ta ce,"to kaima ka ci." ya ce,nima ke zaki bani."ta sunkuyar da kai don kunya sannan ta dauka ita ma ta soma bashi. sai da suka yi dam.sannan ya ce mata kije kiyi alwala kizo muyi sallah. ta ce ai tun dazun nayi sallah.ya ce wannan ta ma'aurata ce,zamu gode wa Allah taare da rokonshi zuri'a tagari,da kuma fatan ya tsare mu daga sharrin shaidan dama duk abin ki. Ta fita ta dauro alwala,shi kuma ya kuskure baki.shine yaja su sallar,raka'a biu sannan sukayi ta addu'a,shi ne ma yake addu'ar ita kuma tana cewa amin. bayan sun idar da sallah idar da sallar,ya yi mata tambayoyi game da addini ta sanar da shi,yayi mata yan gyare-gyare sannan suka kwanta. sam Abba be daga kafa ba,a ranar ya angwance abin shi.don haka yayi kwanan farin ciki. da asubahi ya dawo masallaci,har lokacin amarya tana ta shirga bacci ya zauna bakin gadon yana kallonta.yasa hannunshi a gefen kumatunta. "sleeping beauty" tayi mika sannan ta bude ido,ya ce"a tashi ayi sallah ko?gashi sai kinyi wanka ko?" ta ce,"eh." ya ce, "to tashi ki gani gari ya soma haske." zani taja ta daura

daura ta nufi waje. da kallo tabi tsakar gidan,sannan ta dawo dakin Abba.bazan iya jan ruwa daga cikin rijiya ba. ya fito da sauri yaja mata sannan yakai mata bandakin,ya dawo yayi taja yana cika robobin ruwanta.sai da ya cika mata komai,sannan ya koma dakin. lokacin ta idar da sallah.ya dauko Alqur'ani mai girma ya zauna gabanta,ya ce "madam zamuyi karatu." ta dube shi tareda yatsina fuska,"wallahi bacci nakeji."ya ce,"daure muyi ko aya biyar ce," ta ce cikin shagwaba,"ni biyu." ya ce,"to bismillah,mu fara ta sama ko ta kasa?" ta ce,"ni kam ko ta ina, don haka sai ya soma mata daga bakara yana yi tana maimaitawa,aya biyu kusan minti ashirin ta ce, "zan kwanta." Ya aje kur'ani ya kmama hannunta,zo muje kicin mu gani me zamu nema.dan dole ta bishi zuwa kicin din.suka tsaya suna kallm kayan, tukwane ne zuwa kuloli da sauran tarkace,sai risho.ta dube shi cikin yanayin tsausaya ma kanta. tace, sun qi sai min gas cooker wai gidana ba flate ba ne bai dace da gas cooker ba. ita ko anti aisha an sai mata, kayan girkita ma duk yan chaina. tausayinta ya tsirga ma abba, ya jawo ta jikinshi ya rungume, kada ki damu bishira, duk abin da a ke sai ma yar gata xan sai miki, matsawar Allah ya hore min. ya janyo kwalin risho din ya ciro shi, ya hada yace xan siyo lagwani da kalanxir kenan ko? tace eh. ya miqe bari na dawo. tace to. ta nufi daki ta fada kan gadanta taci gaba da baccinta, shi kam gidansu ya nufa. tun daga nesa ya hango ahj babba xai shiga dakin waje, in da aka sauki baqi maxa, da alama ahjn ya hango shine shi yasa ya tsaya a bakin qofar. abba yana cike da fara'a ya rusuna xai gaida ahj shi kuma ya miqa masa hannu, dan haka sai abban ya kama suka yi musabaha. ahj yace Alhamdulillahi abbana, ka xama mutun, sai ayi ta hakuri da rayuwa. abba ya sunkuyar da kai yana tambayar kanshi ko manya suna ganewa ne in kayi aurатаyya da matanka? ahj ya katse shi da cewa, ya kwanan iyalin taka? tare suka shiga gun baqin, yana gaida su ya fito xuwa cikin gidan. yana leqawa

dakin umma bata ciki, sai baqi. wata uwani dake matsayin abokiyan wasansu tace ango amarya ta koro ka ne? yace, keni karki dame ni, ina umma na? umma daga kicin tace, gani nan dana, xo qyale su uwani. gurinta ya nufa yana cewa,kina kicin ashe? tace, eh ina hada ma baqi abin kari ne. yace kalli yanda duk suka yi mana kaca kaca da gidan,wannan in sun tafi sai kin sha aikin tsaftace gidan.tace to yana iya?dole in gyara in sun tafi,ai arxiki ne ma xuwan nasu.abba yayi dan murmushi,sannanya canxa maganan da cewa,umma galan din kananxir muke so.tace,ga ma kananxir din can da ahj ya siyo jarka babba wai saboda biki.nace yaushe girkin biki xai yiwu da kananxir?shine na aje shi.sai kadau galan ka cika.yayi murmushi. Yace kai ahj akwai qoqari, musamman Ikcn bikin nan.umma tayi yar dariya tare da cewa ko abinci fa baya iya tsayawa yaci,in na masa magana sai yace bijin da guda ina yaga ta cin abinci?abba ya girgixa kai,Allah ya rama muku da mafificin alkairin da kuke min,yasa ni ma in goya ku kamar yadda kuka goya ni.tace amin abba ai muma kana yi mana biyayya Allah yasa albarka a cikin auran, ya baka yaya masu binka kaima.yace amin. ya isa gida da kalanxir da lakwani ya samu ta koma bacci,dan haka ya hada ya dora ruwan xafi ya juye cikin plaks yaje ya ce ta shi mu karya. tayi juyi tare da cewa sai an jima,dama tun jiya sun shigo da biredi da kayan tea,shima sai ya sake kwanciya.ya mannata jikinshi suka koma bacci,goma da ishirin wayarsa ta tashe shi da ruri. ya daga ahj ne ke san ganinsa qarfe sha biyu.yace,ya sanme shi can kasuwa,ita ma ta tashi.nan suka karya sannan yayo wanka ya tafi kiran abba.kaya ne ya ba shi da kudin mota, yace ya kawo ma baqi yan xamfara da xasu koma gida yace ka tabbata ka dauki shatar mota har Zamfara abba ya ce to.sai da ya samu motar sannan yaje ya loda su suka daga,suna ta godiya.yau satinsu daya cir umman shi ke kai masu abinci,sannan ita kuma ya shigo da kayan marmari,sai kaji ko tsire da balango.abba ya

shirya tsaf cikin qananan kaya xai tafi shago,yace madam yau fa abinci xaki yi mana,kin san abokaina su ahmad xasu xo muci abinci,in yaso daga nan sai mu wuce gaisuwan surukai gidanku a matsayin kina amarya wanda xaki soma girki yau, me xaki dafa mana? ta tashi xaune duk abin da ka ke so.dadi ya rufe shi,kowanne dai ki mana fatana shine ki birge abokaina.tace an gama. yace to bari inje xan turo yaran shago da abinci da cefane tace to, har ya tafi kuma ya dawo yace, xan biya in turo miki ummi,tace saidai in fati.yace,ummi tafi fati hanxarin aiki fa.tace eh nafi son fatin.kamar kullum sai da ya soma shiga gun ummarshi suka gaisa ta tambaye bishira, yace lafiyi lau.yaci gaba da cewa, yau nema xata soma girki,nace na turo mata ummi tace wai fati.umma tayi murmushi, sannantace kai ko yaushe xata so a tura mata ummi umma tace ina xata so a tura mata ummi? ita fa ba natsuwa gareta ba.abba yace, duk da haka tafi fati hanxarin aiki. umma tace,yanxu dai tura mata fatin.ka ko sai kayan abinci?yace ina fa,yanxu dai xan je bin wasu yan kudadena.tace ina xuwa baqar leda ta ciro a cikin adakan suturunta,taxo ta xauna sannan ta umurce shi da ya xauna.ta miqa mashi ledan tace,kwance ka gani.abba ya kwance ledan yana cewa menene a ciki ummana? kudin da yayi arba da su su suka bashi amsa yace,umma kudin nan fa?tace gudunmawa ce da jama'a sukayi ta bani,ka gansu nan.yanxu ka je ka siyi kayan abinci da su.abba yayi dariya, sannan ya kullesu ya miqa mata tare da cewa. Allah ya kyauta in amsan makh kudi, ki boye abinki. tace bana son muyi ta jan magana abba,kawai ka riqe kudin nan.muryan tsohuwa ne ta katse su,inda take cewa yanxu ke suwaiba hakan da ki ka yi adalci ne? yar gudunmuwar da ki ka samu kiba mai sunan malam duka, ummin fa? umma tace,to tsohuwa ummi me xatayi da kudi yanxun?abba yace kai wannan matan sa idan ki ya gota misali. Tace kai tafi can,ni rufemin baki,ke kuma suwaiba da kike cewan haka ba kya siyan mata yan tukwane da kwanonin nan na yayi

maigida cika duba ne ku ke ce musu ko ci bari kallo? umma da abba suka sa dariya,tsohuwa ta sake jin haushi ta ce eh dole ku min dariya tunda kema kin xama shi,ai sai kiyi ta bashi naki ne ba nawa ba.umma tace yi haquri tsohuwa, gani nayi nan gaba muna sa ran abba shi ne xai ma ummi kayan dakin ma gaba daya tace,me kika ce?tab mai sunan mlm ne xai yi wa takwara wani abin axo a gani?shi da ya tsaneta.abba yace,in lkcn yaxo ke kya yi ma.ta tafa hannu cikin jin matuqan takaici ta ce,a gayawa mai xuciya ba mai dukiya ba,dan ko xan mata.ta nufi dakinta tana fada.umma tace,tashi abba,dauki kudin nan kaje. yace,wallah umma bari dai in dauka tunda kin matsa,amma ba xan amsa duka ba.ya qirga dubu uku,tace ka qara dan kusan dubu tara ne kudin,yace haka ma ya isa ki adana sauran.tace shi kenan. daga nan kasuwa ya wuce,ya sai kayan abinci.bayan ya amso wadansu kudaden shi ya hada ya kai mata. Sannan ya yi cefanen kayan miyan rigijif da nama ya aika yaran shago.dama kafin ya bar layin ya shiga gun umman bashir ya gaisheta.da tana ta bace bacen rai,sannan da yace umma ina fati? taje xata taya bishira aiki ne.sai ta washe baki,tan bandaki. yace to in ta fito ki tura mata ita.ya fice abinshi.biyu saura ya iyo gidan,tun a tsakar gidan yake jin qamshin shinkafa.ya isa kicin din tuni ta sauke shinkafa sai miya.yace ki xubama yaran shagona.ya dubi fati da ke yanka latas yace,in kin gama jamin ruwan wanka a rijiya.tace to.yana daki yana sa kaya yaji sallamar abokanshi.da sauri ya fito, suna ta yi masa tsiya ango kasha gyara, munxo dibar girki. abba ya bude musu falo,falan yaji jeran samiru abin yayi na xamanin, ga kujeru suka xauna suna yaba dukiyar da aka xuba cikin falon.ya fito yace bishira ta saka hijabi taje su gaisa.ya dauki abinci ya kai musu,sannan yasa fati takai filet da ruwan sha,shi kuma ya koma daki dan qarasa saka kaya.a xatam shi xai samu sunyi nisa da cin abincin amma sai me? dukkansu su shida kowanne filet din gabansa shaqe da abinci da nama,ga cokali a

hannunsu,amma kowannansu juya abincin yake,yace a,a kuci mana kai muke jira ka bude da addua.tsaki yayi, yasan halin ahmad gun xolaya,dan haka sai yace muktar kuci abincinku,in kun bi ta ahmad xai ta bata mana lkc.cokali ya dauka shima ya xauna kusa da sunusi ya ce mu ci tare.take ya yatsina fuska tare da dawo da abincin ya xube shi kan ledar yana tande harshansa.dan danan gishirin da ya kama masa harshe ya ragu,cike da kunya ya dubi abokanan nasa suna ta dariyar da suke gimtse.da farko ya dubi sunusi,wai gishiri ka qara ne?sunusi ya ce,qila dai gishirin nan da bakin buhu ta xufa.muktar yace dubi gaban rigata ni da shegen kwandayi na tura nama a baki na tauna ya qwace saboda tsananin qarfi ya dawo ya fado min jiki.abba ya miqe cikin damuwa ya ce bari in maku wata miyar. ahmad yace a,a duk yunwa muka debo, inda yaji da mai a bamu muyi maneji. abba ya fito xuwa kicin.fati ce xaune da nata abincin tana ta juya cokalin. Abba yace ina bishiran?taje daki.ya daga murya ya kirata,ta amsa sannan taxo.ya dubeta fuska a daure ke dama ba ki iya abinci ba shi ne ki ka toxarta ni cikin abokaina?maimakon ki fada min? tace, to ai fati ce nace tayi miyar, danni bansan yadda a ke yi ba. haushi ya kama shi.ya dubi fati, ke dama baki iya komai ba kema?shashasha, gara ki koyi girki, dan duk macen da bata iya girki ba ba mace ba ce.ya daka mata tsawa, tashi kije gidan ummana ki ce ta baki abinci inji ni,ni da abokaina ne.sallamar yaron shagon shi ne ta katse shi,ya gaishe su sannan ya ce,naxo daukan abincin.ya dubi bishira,kina da yaji?tace,eh gashi can cikin kwalba da ummanka ta aiko min.ya ce,xuba ma yaran nan yaji da mai.ta ce ai akwai miyar.yace miyar ai ta xama guba.fati ta dauko abinci cikin kula xata fita,yace wannan fa?ba aikenki nayi ba? tace na ummanmu ne xan tafi mata da shi,ita ce ta ce duk abin da a ka dafa inxo mata da shi, shi ne yaya bishira ta xuba mata.abba baice qala ba, sai al-ajabin halin uwarshi ya ke yi. Bishira ta ce, kawo ita ma a kwashe miyar a xuba mata mai da

yaji. ya daka ma fati tsawa,kai mata haka ni ki dauko min abinci gun ummana, minti uku na baki in kin wuce biyar xa ki sani.da gudu ta fita tana shiga gidansu ta aje bata tsaya yin surutu ba, ta fita da gudu.dan wake umma tayi,Allah yasa tayi da yawa,dan haka ta xuba musu ta dora ma fati ba tare da ta tambeyeta dalilin aikowarshi ba. sai dai a ranta tana ta saqe saqe tace,qila sun fasa girkin ne,ko kuma bai kai kayan abincin ba.koda fati ta kai musu dan waken nan suka baje suka kwashi dan wake suna santi.bishira tana jiyo shewarsu.abba na cewa ummana ta iya girki, bari in xo in sa muku waigi.muktar yace, ka kai amaryarka ta koyo girki.garzali yace,saboda irin wannan matsalan kafin in auri yarinya sai na tabbata ta iya girki.ahmad ya ce daya daga cikin illar auran yaqan masu kudin nan kenan, sangartattu ne basu iya komai ba tun da a gidajensu ba sasu a ke yi ba.ado yace wasu ba amma wasu suna saka yaransu.
vels / ZURFIN CIKI book 1 part 7
ZURFIN CIKI book 1 part 7
Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 21:59
Ado yace wasu ba, amma wasu suna saka yaransu,dan wani abokin wasanmu a kaduna ya auri yar wani attajiri, ba kaga girki ba kala kala.abba dai yana ta binsu da ido,har aka yi kiran sallar la'asar suka fita xuwa masallaci,daga can xasu wuce gaida surukai.bishirata dinga jin haushi,wai abokan abba sunxo har gidanta sunci mata xarafi.ummi ta fito dan xuwa gidan su amina,domin akwai wata xainab da wai ta musu gulma xasuje su.kirata har gida su dake ta.suna xuwa kuwa suka tsaya a waje suna tunanin yadda xa suyi ta fito,amina ta ce muje mu ce mun xo gunta ne, inta xo rakiyan mu mu duke ta mu gudu.haka kuwa suka yi,har ummarta tana ba su quli quli,ita ga me qawayen yan tana rako su tun daga soron gidan suka soma dukanta.sai da ummanta ta fito sannan suka gudu.ta ce yar tata kin san gidansu?xainab tace,na sani.ummar tata ta taso ta.su kuwa su ummi suna fitowa sai suka canxa hanya.amina tace dan allah muje gidan

amaryan abbanku,naji ana ta labarin jeranta an ce kaya ne na uban gari. . Ummi ta ce,"duk da son kirgan samirana ban taba zuwa ba,saboda na kula ita ma yar rainin wayau ce kamar mijinta." Amina ta ce,"ke dai muje inga samirun da aka ce jajaye wai masu shida-shida" ummi ta ce,"mu fara bi ta shagonsa in yana nan to sai muje,in ko bayanan ba zani ba ya dake ni a banza." duk da cewa shagon da gidan tsakaninsu da nisa sai da sukaje suka duba sukaga yana nan,sannan suka je. gidan shiru sunata sallama,ummi ta nufi wata kofa ta tura,ta yafito Amina,"zoki gani nan ne falon."suka kirge samiru tsaf,sannan suka fito. ta window ummi ta leka nan ta hango bishira kan gado tana ta bacci,suka je kicin suka leka suka tura dayan dakin da ba kowa. nan ma sukaga ba komai ciki,an dai shimfida ledar kasa an sa manyan robobin ruwa. suka fito,ummi ta ce,"gaskiya matar nan banza ce,dubi yadda mukaje tana ta bacci." daga can suka sake zuwa gidan wata amaryar don kirga samira,sai kusan magariba sannan ta shiga.umma tana alwala ta ce,"to tunkiya uwar tumbele,tun yaushe ki ka bar gidannan sai yanzun kika waiwayo? sai kararki da jama'a keta kawo min?to na gaji da halinki,bari Alhaji ya dawo,wato tunda yanzu babu Abba a gida shi yasa iskancinki ke son yafi da." tsohuwa ta fito,"suwaiba da a ce ba a gabana kika haifi takwara ba,to da zance ba yarki ba ce,ba dama yarinya ta fita wasa?" umma ta ce,"ban hanata yin wasa ba,amma tayi shi a gida yawo ne bashi da dadi." tsohuwa ta ce,"a'a karki wani fada ma Alhaji,ta daina ko takwara?" ummi ta ce, eh.umma dan haushi ta shige daki ta barsu anan. lokacin da su Abba suka je gidan surukanshi an amshe su ba yabo ba fallasa,har ma da zasu tafi aka basu (uniforms)din bishira na boko wai ranar monday lallai ta tafi makaranta. sun zaga gidajan danginta dake kusa,sannan suka dawo gida.ya sameta tana fushi,shima shareta yayi don yaji haushi barnar abincin da tayi masa. dadin dadawa gidan nan yanda ya bar shi haka ya tadda shi.ita kanta batayi wanka ba

ta kwanta tana ta uban bacci.fita yayi daga gidan,sai goman dare sannan ya shigo ya rufe gidan yaja ruwa yaje yayi wanka. sannan ya shiga dakin,tsayawa yayi yana kallon gadon mutsu-mutsu,sannan ga kaya nan duk a kai.ita kuma tana kwance rike da wani littafi tana karantawa. . Ya ce,"bishira wai me yasa bakya son kakkabe gadonki? ta dube shi nifa duk na gajine.tsaki yaja tare da cewa me kikayi da har kika gaji? bani guri ni in gyara shimfidar zan kwanta. shine ya kakkabe shimfidar sannan ya kwanta.duk da ya cike da bukata amma haushi ya hanashi kulata,sai ma baya da ya juya mata. Abba yanada tsafta sosai,haka nan ma'abocin son kamshi ne,duk da gyara gami da tsafta irin na ummanshi wata ran har cin gyaranta yake yi.sam baya so yaga ko ina rakwacan,yafi son komai ya ganshi a muhallinsa. dole kullum shi ke share gidan ya wanke ban daki,sannan da rana in ya dawo ya dora abinci. litinin duk makaranta suka koma daga dogon hutun kirismeti da suka samu.Abba ya koma kan aikinsa na bautar kasa.dan haka kusan tare suka fita da bishira ta wuce makaranta shima ya wuce wurin koyar war shi. . Ya rigata dawowa gidan,dan haka gajeren wando ya samu ya shiga tsabtace gidan.sannan ya dora dafa dukan taliya. uku da minti sha biyar ta shigo ya dubeta ina kika tsaya? ta ce,ba ko ina mufa makarantar mu biyu da rabi ake tashin mu.dan ma na samu direban gidanmu da yazo daukan kannena shine ya kawo ni. Abba y sake had'e rai,motar gidanku? Bn baki kud'in mota ba?Ta ce ka bani, ya ce to bn amnce ki sake shiga motar gidanku ba. Ta ce,"kan me ? ya harare ta ba tare d ya bata amsa ba,y nufi kicin tabi bayanshi d harara,sannan ta shige d'aki. A ganin Abba sam babu wani sauki da ya samu a auranshi,nashi ganin wahala ya d'ebo ma kanshi,kwanciyada ita ne kurum zai ce ya k'aru d shi acikin auren. Ya shiga gidansu d sallama,Umma ta amsa tana zaune kan sallaya bayan ta idar d sallar Isha'i. Ta ce,Abba ba a je an kwanta ba?ya zauna tare d d'an jan tsaki ta

ce,A'a ha,jikin ko garin? Ya ce,Umma gaskiya ni abubuwa sun cud'e min,yarinyar nan tunda a kawo ta sam ban huta ba. Umma ta saki dariya "ka ji Abba d wani zance,dama ce maka a ka yi ana bauta d hutu? Aure shi bautane. Ya ce,Tsaya kiji fa ummata,kinga tun Asubahi in nayo Sallah zan hau sharar gidan,in shirya in je gurin d nike koyarwa. In dawo in dafa abnci,sannan in tafi shago kuma don takaici in na zo kwanciya ni zan kakka6e shimfid'a,ita bata iya komai ba ashe daga gidan nasu.Ni fa har ta soma sure min...... "Kai Abba! Umma ta katse shi d sauri, kada in kuma jin wannan furucin, kana hauka ne?yanzu d fada min menene matsalarka?in dai abnci ne ka bari zan diga aiko muku da shi. Ya ce umma ya ya ma za a yi haka?Tab ai ba zai yi wu ba,Ta dai zo ta koya sati d lahadi. Umma ta ce,To shi kenan,tazo din.kayi ta hkr Abba,nasan ka kai ma d zuciya,don Allah kada ka sake in ji wata fitina,ka lalla6a matarka kuyi zamnku lfy. Abba ya ce, To ko da ya sanar d Bishira cewa yana son taje gurin ummansa ta koyo girki,sai ko ta tuma ta ce ita ba zata je ba,dama dai gurin umman Bashir ce, Ya ce,shi kuma gurin ummansa ya turata,koda Asabar din tazo kin zuwa tayi,shi kuma sai ya shareta ta ya daina girkinki. Sai dai yaje gidn ummanshi yaci,hatta ranar litinin d suke d makaranta bai dafa abncin ba da ya dawo a galabaice da yunwa ta iso. Bashir ya ce, Ni har fata nake wata rana 'yar sa' in'sa ta hadu ku umma,wlh in mata shegen duka. Bishira ta ce,Ni dai bata isa ba, in ma ita ce ta turo shi dn in dinga zuwa gidnta to ba zanje ba. Haka suka yi ta zagin umma,daga bisani Bishira ta mike ta tafi dn kada ya dawo bata nan. Rashin iya girki ya kawowa masoyan 2 rashin jutuwa,wanda ko magana Abba bai cika yi mata ba. In ta zauna tayi ta kuka tana mmk,me ta mishi ya juya mata baya dan da nan? Yau kam abn ya yi kamar kaurace mata ya yi daga dakin baccinta, ya dauki filo ya tafi falo ya kwanta. Tayi ta kuka. Kasa jurewa tayi ta mike ta bishi,kwankwasakofar tayi kusan sau 3 ya ce "Waye?" cikin muryar kuka ta

ce, Ni ce, Abba don Allah ka bude. Ya kunna wutar falon,sannan ya bude ta shigo ta zauna kusa d shi, ta ce, Abba wai mi na maka ne ka tsane ni? ka duba fa ko wata daya ban rufa ba,kasan dai yadda a ka yi auranmu yanzun in Mahaifana suka ji dariya za su Min. Amma ba komai sai biredi ta samu ta k'asuma,d ya tafi shago sai ta yafa mayafinta ta nufin gidn umman bashir. koda tai sallama umman tana kan turmi zaune suna ta ganzar rake ita d su bishir. umman Abba ce ta aiko musu da shi don rashin Adalci suna sha suna yi da ita. Suka shiga lale d zuwan Bishira, ta kalli bashir 'Ina fushi da kai, shine wato har yanzun ba ka zo ba ko? ya ce, Tab, sau 2 ina zuwa zan shiga gidan sai yaya Abba ya fito ya ce min kina bacci, na gane nufinshi baya son ina shiga masa gida,shi yasa na share.Bishira ta ce Um, wannan Yayan naka halinshi sai shi, yanzun ma fa fushi yake dani. Umma ta ce," A kan Me kuma? wai shi dole sai nazo gurin ummarshi na koyi girki, ai ko nace wlh ba ni zuwa. Umman bishir ta rafka salati. sannan tace 'Naga ta kaina ni Sahura,kai Allah ya isa tsakanina d Suwaiba. yanzun kuma ta gama d ni ke ta sako a gaba, so take ta shiga tsakaninku?' Abba ya kura mata ido, yasan abn d ta fada gaskiya ne ya ce "Me na miki to?" ta kalle shi,"Ba ka ma san abn d kayi min ba?Ta ga daya yanzun fa kaurace min kayi. Ya ce ba kya gyara gadonki,ni kuma na gaji d gyarawa. Ta saka tafin hannunta cikin nashi zo muje in gyara. Tausayinta ya ji,ya tashi ya bita yana kallonta duk kakarin d ta yi dn t gyara ta kasa. Sai dai shi ne ya gyara, Sannan ya janyo ta suka kwanta.Sam bata d gardama ko nuna gajiyawa a gurin ba shi hakkinshi na kwanciya. In zai zo sau nawa ba ya damunta,gurin da ta ke birge shi kenan. Amma ba wannan ba ne kadai namiji ke bukata,Musammanirin Abba dan kwalisa. Wata ranar Jumma'a bayan sun tashi daga mkrntr da ya ke koyarwa,ya ce da Ummi ta jira shi zaya aike ta gida. Kudin cefane ya bata ya ce taje ta sai kayan miya d nama ta kai gidanshi, Sannan

ta tsaya tayi masa miyar tare d yi masa sakwara.
. Shi kuma zai je ya fada ma umma, dn yana son d dunkunan wata amarya d yake son karasawa ummi ta zun6uri baki bayan ta amshi kudin ta wuce tana yankun-kunai, ya ce "Ke!" ta waigo "Zo nan . ta dawo, Ya kama mata kunne, Kin san kwana 2 bn ta6a lafiyarki ba ko?to kiyi abn d yau zaki gwammace ba ki zo duniya ba. ya rankwashe mata kai, Sannan ta wuce tayi ce fanan ta nufi gidn Matar gidn tana zaune d kayan mkrnt a jikinta,,Ummi ta mata Sannu harara ta zuba ma Ummi, Ummi ko ta rama,sannan ta ce "Mijinki ya ce in zo in yi mashi sakwara d miya. "Bishira ta ce, To sai ki koma gidn ubnki ki dauko tukunya d murhu b dai nawa ba, Ummi ta ce, To ni dai gaskiya d ubana ba. Bishira ta taso tana cewa Sai na wa? Ummi ta ce, Oho,amma ba nawa ba. Za ta kai mata duka ta goce ta ajiye mata kayan miyan ta ce " Gashi sai kiyi, kila ma baki iya girki ba ne. Taje ta fadawa umma, Umma ta ce "Ke ummi karya ki ke daga zuwa zata hauki d zagi sai ka ce Mahaukacciya? To kije ki fada wa Abban in ya so sai kuje tare ya fada mata amma fa kada ki ce masa ta zage ki, ki ce masa dai yazo ya fada mata zaki tayata. Ummi ko kyn mkrnt ba ta cire ba ta nufi gurinshi,yana tsaka dinki taje,Ummi sai ce masa tayi ta ce ba zam mata girki d tukunya ba. Ya ce Muje gidn ganin nan. "a kofar gida ta zauna tana jiranshi, sai d y shiga sannan ta bishi. Tana tsaye tsakar gida tana jin rigimar d suke yi.Bishira ta dage ita fa babu mai yi mata girki d kayan aiki, shi kuma ya ce tunda ba a koya miki girki ba a gidnku dole ne in sa kanwata ta mini. Ta ce ya turo Fati mana,wannan maran kunyar yarinyar mata tarbiyya ba za ta zo mata gida ta zage ta ba. Ran Abba ya 6aci, ya ce Ga ki nan mara tarbiya,ina fada kina fada ina matsayin mijinki.,Ummi tafi ki tarbiyya domin uwar d ta bata tarbiyya ita ta bani har ki ka amince ki ka aure Ni. Ta ce, Ta baka tarbiyya ko ta asirceka? Ta mallake ka har baka ganin Mahaifiyarka d gashi sai ita. Zancen ya soki Abba sosai Har ya

daga hannu zai mareta sai kuma ya fasa,ya juya ya fita. Fatanshi Allah ya sa ummi bata ji ba,dn yasan tsaf sai ta fada ma Umma. Tana zaune gefen rijiya ya nufo ta,Ummi ina kayan Miyan? tana nuna masa su tare d cewa 'Gasu ya ce,Dauki ki kai ma ummana. Har ta kai bakin kofa ya sake cewa "Ummi!"ta tsaya ya zo ya kalleta Ummi kin ji me Bishira ta ce? Ummi ta dube shi cikin ido,,sannan ta kalli hanyar fita. Naji duk abnda ku ka ce,Ya lumshe ido "Ummi dn Allah ka da ki fad ma Umma. Ta tsura mashi ido,bata ta6a jin Abba ya yi mata magana cikin tattausar murya ba sai yau tunda ta taso. Ta ce, "To." Ta juya, yasa ke cewa Ummi. a waiwayo Don Allah kin ji? kai kurum ta daga sannan ta fita Tafe take tana Mmkn me yasa Abba baya son Umma taji zagin da Matarshi tayi Mata? Hakika d taso Sanar da Umma amma yanda ya yi 'yar Murya yana rokonta sai t jure,koda taje gida bata sanar d Umma ba. Cewa tayi kawai ya ce a ma barshi sai dai cikin ranta ta tsani Matar Yaya Abba fiye d tsanar d ta yi wa Abba. Shi kuwa Abba duk wata hulda tsakaninnshi d matarshi ya dakatar d ita,saboda yana son nuna mata matsayin umma a gurinshi. In ya fita tn Asubahi bacce ke kawo shi gidan,wanka ma cn gdn Umma yake yi sai ya ce mata Bishira tana mkrnt. A cikin rana t 3 hnklnta y gama tashi,taje t fadawa umman Bashir,ta aiko yaje tayi ta fadan gami d zazzagnshi,ya bata hkr y fita. Amma sam Bishira, bai canza mata ba. Sai ma sabon salon d ya dauko na yn kaura daga falon zuwa dayan dakin d babu kowa,dk kayn sawanshi y tattara y koma can. Abba yana d zcy g taurin kai,Umman Bashir ta ce,"Yanzun in kin samu saukinshi to uwar goyonshi ki ka fada mawa, km gwada ki gani za ki gane ta fini a gurinsa. Sannan ki g aikin asiri. . Shi kuma zai je ya fada ma umma, dn yana son d dunkunan wata amarya d yake son karasawa ummi ta zun6uri baki bayan ta amshi kudin ta wuce tana yankun-kunai, ya ce "Ke!" ta waigo "Zo nan . ta dawo, Ya kama mata kunne, Kin san kwana 2 bn ta6a lafiyarki ba ko?to kiyi abn d yau zaki gwammace

ba ki zo duniya ba. ya rankwashe mata kai, Sannan ta wuce tayi ce fanan ta nufi gidn Matar gidn tana zaune d kayan mkrnt a jikinta,,Ummi ta mata Sannu harara ta zuba ma Ummi, Ummi ko ta rama,sannan ta ce "Mijinki ya ce in zo in yi mashi sakwara d miya. "Bishira ta ce, To sai ki koma gidn ubnki ki dauko tukunya d murhu b dai nawa ba, Ummi ta ce, To ni dai gaskiya d ubana ba. Bishira ta taso tana cewa Sai na wa? Ummi ta ce, Oho,amma ba nawa ba. Za ta kai mata duka ta goce ta ajiye mata kayan miyan ta ce " Gashi sai kiyi, kila ma baki iya girki ba ne. Taje ta fadawa umma, Umma ta ce "Ke ummi karya ki ke daga zuwa zata hauki d zagi sai ka ce Mahaukacciya? To kije ki fada wa Abban in ya so sai kuje tare ya fada mata amma fa kada ki ce masa ta zage ki, ki ce masa dai yazo ya fada mata zaki tayata. Ummi ko kyn mkrnt ba ta cire ba ta nufi gurinshi,yana tsaka dinki taje,Ummi sai ce masa tayi ta ce ba zam mata girki d tukunya ba. Ya ce Muje gidn ganin nan. "a kofar gida ta zauna tana jiranshi, sai d y shiga sannan ta bishi. Tana tsaye tsakar gida tana jin rigimar d suke yi.Bishira ta dage ita fa babu mai yi mata girki d kayan aiki, shi kuma ya ce tunda ba a koya miki girki ba a gidnku dole ne in sa kanwata ta mini. Ta ce ya turo Fati mana,wannan maran kunyar yarinyar mata tarbiyya ba za ta zo mata gida ta zage ta ba. Ran Abba ya 6aci, ya ce Ga ki nan mara tarbiya,ina fada kina fada ina matsayin mijinki.,Ummi tafi ki tarbiyya domin uwar d ta bata tarbiyya ita ta bani har ki ka amince ki ka aure Ni. Ta ce, Ta baka tarbiyya ko ta asirceka? Ta mallake ka har baka ganin Mahaifiyarka d gashi sai ita. Zancen ya soki Abba sosai Har ya daga hannu zai mareta sai kuma ya fasa,ya juya ya fita. Fatanshi Allah ya sa ummi bata ji ba,dn yasan tsaf sai ta fada ma Umma. Tana zaune gefen rijiya ya nufo ta,Ummi ina kayan Miyan? tana nuna masa su tare d cewa 'Gasu ya ce,Dauki ki kai ma ummana. Har ta kai bakin kofa ya sake cewa "Ummi!"ta tsaya ya zo ya kalleta Ummi kin ji me Bishira ta ce? Ummi ta dube shi

cikin ido,,sannan ta kalli hanyar fita. Naji duk abnda ku ka ce,Ya lumshe ido "Ummi dn Allah ka da ki fad ma Umma. Ta tsura mashi ido,bata ta6a jin Abba ya yi mata magana cikin tattausar murya ba sai yau tunda ta taso. Ta ce, "To." Ta juya, yasa ke cewa Ummi. a waiwayo Don Allah kin ji? kai kurum ta daga sannan ta fita Tafe take tana Mmkn me yasa Abba baya son Umma taji zagin da Matarshi tayi Mata? Hakika d taso Sanar da Umma amma yanda ya yi 'yar Murya yana rokonta sai t jure,koda taje gida bata sanar d Umma ba. Cewa tayi kawai ya ce a ma barshi sai dai cikin ranta ta tsani Matar Yaya Abba fiye d tsanar d ta yi wa Abba. Shi kuwa Abba duk wata hulda tsakaninnshi d matarshi ya dakatar d ita,saboda yana son nuna mata matsayin umma a gurinshi. In ya fita tn Asubahi bacce ke kawo shi gidan,wanka ma cn gdn Umma yake yi sai ya ce mata Bishira tana mkrnt. A cikin rana t 3 hnklnta y gama tashi,taje t fadawa umman Bashir,ta aiko yaje tayi ta fadan gami d zazzagnshi,ya bata hkr y fita. Amma sam Bishira, bai canza mata ba. Sai ma sabon salon d ya dauko na yn kaura daga falon zuwa dayan dakin d babu kowa,dk kayn sawanshi y tattara y koma can. Abba yana d zcy g taurin kai,Umman Bashir ta ce,"Yanzun in kin samu saukinshi to uwar goyonshi ki ka fada mawa, km gwada ki gani za ki gane ta fini a gurinsa. Sannan ki g aikin asiri. . Bishira t nufi gurin umma t same t zaune tana yankan ku6ewar miya. tun d a ka kawo ta yau ne rana ta farko d ta zo. Umma ta ce, "A'a Maraba d Bshra. shigo koda yake je ki gaida tsohuwa. Taje suks gaisa,Tsohuwa ta ce Ke dai wannan yarinyar kirkinki d sauki,a ce tunda ki ka zo unguwar nan baki ta6a zuwa kin gaida iyayensa ba? Umma t jiyo 6aram6aramar d Tsohuwa ke yi,d sauri tazo ta ce Tsohuwa b laifinta ba ne, laifin Abba ne. Ba sai ya kawo ta ba za tazo? Jin haka Bishira ta samu bakin magana,wlh Tsohuwa laifinsa ne nayi in zo ya ki,yanzun hk kararsa na kawo. in y fita tn Asubahi sai dare bana sanin shigowarshi. Yanzun ni tn jiya ma bn sa shi a idona ba,Umma

ta ce Shi Abban ne ke hk? Ta ce IIlahi kuwa, ni bana son in je gidanmu in kai karanshi ne amma shi baya gani,yanzun fa ya tattare y koma dakin nan d ba kowa. Ran Umma ya 6aci, a irin tarbiyyar da ta yi wa Abba bata zaci zai wulaqanta mace ba, . Ummi tana shigowa daga Islamiyya ta ce,maza d sauri shagon yayanki kira mn shi. kan keke ta same shi yana t dinki, t shiga d sallama,sauran yaran shagon ma suna t dinki,ta ce yaya Abba Umma ta ce kazo yanzu. Ya dube ta me ya faru?Ta girgiza kai,bn sani ba, ta dai ce kazo. Take ya mike,ita km t fice d gudu. A ranshi ya ce ko yaushi Ummi zata yi hnkl t dinga tafiya irin t mata? Yana shiga gidn umma t rufe shi d fada,ba tare d tambaye shi dalilin shi na yi wa matarshi abn d yake mata ba. Ta ce,"Maza gata nan dakin Tsohuwa kaje ku koma gida ka bata hkr. kanshi na kasa bai ce kala ba ya nufi dakin Tsohuwa. Ya dube ta Tashi muje. Har daki suka shiga ya dube ta kiyi hkr. Ta ce, To nima kayi hkr. Ya ce kin ga matar d ki ke zagi ta baki gaskiya alhalin danta nake fushi. Ya ce ki kula kici albarkacinta karki sake ki km fadin wata mummunar magana a kanta,km hucewar da nayi da hkrn d na baki kada ki zata dn kin isa ne,umurninta na cika,ta ce to na daina. . Da dare gidn Umma ya je ya bata hkrn dn yaga ta dau zafi, ya ce, "Umma yarinyar nan bata kyautawa, abn d take min ni d har zan kai wa yarta kara na gaji. Umma ta ce, kada ka soma,kayi t hkr in girkin ne matsalarku tunda bata son tazo ta koya kai ai ka iya,sai ka ware lkc ka zauna ka dinga koya mata kasa tayi kana kallo har ta iya. Ya ce To, amma kin huce kin daina haushina,? Umma ta ce , sam ban jin haushinka Abba raina yana 6aci ne in ji an ce ga laifinka, ya ce to na gode ummata. Shawarar Ummanshi ya dauka,ranar farko ya ce ta dora farar shinka fa sai da ya koya mata yadda zata dafata kashi-kashi,harkala 4. Sannan ya ce,tayi jajjage tayi tana wai-wai ita duk ta gaji. Yana gefe zaune d wayarshi yana ta Game sai d yasa ta tayi miyar komai yana nuna mata yadda zata yi. Sai gashi kafin wani lkc

Bishira ta iya girki, gurin tuwo ne a ka danfi
samun matsala,sukai kwana 4 suna yi yana
gudaji. . Yanzu sun samu jituwa dk d dai abncin
ma ba ya samunshi kn lkc sai dai kuma fannin
tsafta.Duk da yakan zage ya gyara gidn d shara
kullum in ya dawo Masallaci ya wanke bayi
fes,cikin dakunan a nan matsalar take, sannan
jikinta ma bata son gyara shi. Cikin haka ta kamu
d laulayin ciki sun je asibti sun samu magunguna
dk d hk amai ko ruwa tasha sai y dawo, dk hnkln
Abba ya tashi y kira wayar Anti ya sanar d ita.
Da dare tazo dubata ita d mijinta suka zo,sun
same su Abba yana bata tea,ganin Anty,Bishira ta
soma kuka wai ita zata bi Anty. Anty ta ce A"a ki
zauna ga mijinki na kula d ke, ni dai bana zama
in kin je gidana ba zai miki dadi ba. Sunyi Murna
d Abba ya fada musu ciki ne, take Anty ta kira
Mahaifiyarsu ta fada mata. "Tabdi!" in ji hjy. tun
yanzun? To Allah ya raba lfy. Anty ta ce to sai
anjima,dn jin yadda hjyr bata yi murna d cikin ba,
km bata so Abba ya gane. Ta dubi Bishira, Momy
ta ce a gaisheki d jiki, Bishira ta ce ba za ta zo
ba?Rannan d muka yi waya d Anty Aisha ta ce
min ita ko Momy taje / ZURFIN CIKI book 1 part 8
ZURFIN CIKI book 1 part 8
Posted by Bashir Sani Fesan on 14 Dec 2016 - 22:01
Ni kuma sai naga ta min qanqanta. Ummi ta ce,
ahj kaima ka sai mota ne mu dinga shiga? ya ce,
to xan siya mamana, ki dunga min addu'a kinji?
umma ta ce, nayi murna abbana, ya yi abin
hawa. bari in je masa albishir. tsohuwa ta taba
baki, sannan ta ce, kullum burinku da tattalinku
na ne sunan mlm ne, ita takwara kun maida ta
baya. umma ta ce, sai na dawo. ta fice, dan
tasan tsohuwa da mita. abba yayi murna samun
abin hawa, domin da dan nisa in da ya ke xuwa,
waton makarantarsu ummi, in ya shirya ya kanxo
gidansu ummanshi ya dauki ummi su tafi. jwanci
tashi su ummi an shiga aji uku, lkcn abba ya
gama service din shi, ya amshi certificate. bayan
sun je sun yi faretinsu. dakin umma ya dire, ummi
tunda ya shigo take kallonshi da kayan yan
bautar qasa. ita kam kayan suna birgeta, ya dube

ta kallan fa? ta dauke kanta, sannan ta murguda baki, umma ta nufi kicin tana dariyar halin ummi da abba. dama ummin tana kwance kan kujera ne tana wasa da wayar umma, yace ta ga me kyau tana ta kallona, ba xa dai ki samu miji mai kyau kamar ni ba. . Ba ta san Ikcn da ta ce, tir, da me kama da kai gara in mutu banyi aure ba. ya dubeta da sauri sannan ya dauki hijab din umma ya jefeta, tare da cewa, mummuna, qaxama gaki mahaukaciya. wama xai aure ki? sai kn mahaukaci dan umanki. ta hade rai tana kallanshi, ya ce daina kallona me kama da goggon biri, in kuma kika min wata magana in xane ki. fuu ta tashi ta shige uwar daki. tana jiyo hiransu da umma, in da yake cewa, naso a ce ummi tana aji uku ne Ikcn da xan bar makarantantan mu bari tare, saboda sam bata ji. gashi akwai mlmn da aka samu a makarantan ma su bata yara, sannan tana da wata qawa da aka kama da wani malami a bayin makaranta. sai da taci duka sannan ta rabu da yarinyar. umma ta daff qirji tare da cewa, na siige su ni suwaiba, to ko amina ce qawan tata? abba ya ce, ba ita ba ce. umma ta ce, hu-um, to makarantar boko dai ba tilas, da yaro ya fada cikin irin wannan rayuwar gara a bar bokm. abba ya ce, ina ganin xan nemi koyarwa a makarantan, in naci sa'a an daukeni to sai ta qarasa har Ikcn. . Abba ya ce Ina ganin zan nemi koyarwa a mkrntr in na ci sa' an daukeni to sai ta ci gaba hr zuwa Ikcn d zata gama,sai in bar koyarwar. Umma ta ce,To hkn za a yi. Ummi km daga cikn dk take mgn ita 1,ta ce Da na shiga 3,ka ci gaba d koyarwa a mkrntrm ko dai ka ci gaba d hn ni sakewa? In yana aji numfashi mai karfi ma bana iya yin shi,Allah yasa kada a dauke ka. Murna kmr me gurin Ummi d taga an yi bakwai 2 Abba bai zo ba,hk na nufin ba a dauke shi a mkrntr ba. . Don hk ta ci gaba d tsula tsiyarta. Kwatam! a sati na 3 sai gashi ya zo daukarta suje mkrnt,hr kuka sai d ummi tayi don takaici. Daga dawowarshi km y dora mata daga in d ya tsaya,d rashin mutunci,hr t soma yi mishi fatan mutuwa,dn tana ganin matsawar

Abba yana raye baza ta ta6a jin dadin rayuwar dny ba. Tunda cikin bishira ya samu t daina zuwa mkrnt, Abba bai matsa mata ba,amma d yaga t soma dan jin dadi,sai ya ce ta fara zuwa. . Haka ta ke zuwan yau taje gobe ta ki zuwa ta ce ba a komai hr lkcn biyn kudi yayi. Duk d tsadar mkrntr hk Abba ya fige ya biya,daga bisani ma sai ta daina zuwa, Abba ya kira Anty a waya ya fada mata Bishira ta ki zuwa mkrnt. Yaya-yayi ta ki,shi km gsky ta zo tayi mata fada,dn ba ya so su momy suga laifinshi., Don ko d suka je gaisuwar surukai sai d ta ce "Kada a katsewa 'yarta krt"Anti ta ce za ta zo. . Ai kuwa ranar d Anty tazo taga ta kaici gidn Bishira,ko ina datti,Falon d ta leka dk kura d yanar gizo-gzo. Cikin dakin baccinsu kuwa ko ina yamutse d kaya,bngo dk t tofe shi d miyau,sannan g wani gwangwani madara gefenta ta kusan cika shi d miyau. Gashin kanta rabi an tsefe shi rabi ba a tsefe ba.jikinta fari sol tamkar bai ta6a ganin ruwa ba. Anty t doka salati tare d cewa Bishira me zan gani hk?Dan ubnki hk ki k dawo? Dubi gdnk?dubu kanki? A kanki a ka soma ciki?nan t zauna ta zageta tas, sannan ta taya t suka gyara gidn suna yi tana fada. Ta ce Hk ki ka ga ina yi a gidana?Ko sauran jama'a hk suke yi? Za ki sa a zagi uwarmu a ce an sangarta ki alhalin aikin gida dk a na sa ku.Sannan kin ki mkrnt,to ki sani kanki zaki cuta dn kuwa dk ranar d mijinki y zama wani abu 'yar boko zaya nema ya tafi d ita cikin lamuranshi. . Zan km hada ki d momy.byn sun gyara gidn t sata tayi wanka t dauki kaya masu kyau t saka. Gwangwanin miyau tasa t tayi jifa dashi,ta ce ki dinga saka sweet ko goro a bakinki zanje nan d sati 1 zan dauko momy muzo tare. kin san dai me zai biyo baya. Abba da ya shigo gdn byn Isha'i dk d cewa dare ne sai d y gane an tsaftace gdn,Domin kamshi tare d iskar da ke kadawa a gdn sun bayyana hk. Dakin ta da ya yi wa kaura yau kam hr bakin gado,ganin t cikin kwalliya yasa shi cikin wani yanayi wanda ya kwana 2 bai shiga ba. Ko abncin bai nema ba,ya shiga caftar Syy,wnd ita ma dk d tana

laulayi tana ra'ayin hkn,don hk sai suka rankaya. Kwana 2 ya dan samu sauki kazantar dn tana tsoron momynsu tazo ta gani,sannan tana zuwa mkrnt. Amma d momyn tazo tayi mata fada t tafi,shi kenan sai ta koma gdn jiya,dama Hausawa sun ce mai hali ba ya fasa Halinsa. Haka dai hr cikin ya tsufa Umma tasa shi ya sayi dk wani abu da mai jego da jaririnta za su bukata. . Ita km ta daka yajin mai jego ta tanadi sabulun salo zuwa Kwallin da za a sa ma jariri. Wani dare Abba y kira Umma,Alhj ne y daga nan y sanr d su bishira bata d lfy,yana ganin haiuwa ce. Alhj d kns y raka umma hr gidn suka buga Abba ya bude,suka shiga.Ranar Alhj y yi burin mota,dmn d yana d mota yanzun sai su tafi assibiti. Bishira bata d juriya,dn hk sai raki take yi,tana fadin a kaita assibiti. A daddafe suka kai 4 dare Ahlj ya je ya taso abokinshi suka kaita assibiti tare d su umma,karfe 8 na safe ta haifi danta namiji. . Umman Bashir d taji sai ta hau fadan me ya sa ba a sanr d ita ba?Alhj karami ya rufeta d fadan cewa,ita wace irin mutum ce? Sam ita bata son Alkairi ba,sannan ya fita ya yi wa Alhj babba barka,dg assibti gdnsu iyayenta suka wuce d ita ba tare d sun nemi shawarar mijinta ba ko ta iyayenshi. Hjy ce ta bada wannan umurnin,rai 6ace Abba ya zo gurin umma dn ita ta baro gurin ne d iyayenta suka iso. Ya ce,"dama umma umma haka akeyi sai a daukar wa mu2m mata a tafi da ita ba tare da neman izini ba?to gaskiya bazan yarda ba." umma ta ce,"ka kyalesu, Allah ya raya.shi kenan, tafiya da ita ba laifi bane tunda ita kadai ce a gidan ba mai kula da ita matsalar dai da basu nemi izininka ba." ya ce,"sai ka ce ba zamana take ba? wankan gidan addini ne?dama fa niyyata in kawo ta nan gidan ki lura da ita." umma ta ce,"to yanxu dai hakuri kawai zan baka,ka bar maganar." tayi ta lallashinsa har dai ya hakura,amma shifa ya dau alwashin sai ya nuna musu nasa ikon. umma ta hada abubuwan data tanada suka tafi da makota.bayan sun shiga gidan aka kai su gefen da maijego take. sun sami

dakin tamkam da jama'a nan dai suka zauna aka gaisa,sa wani gani-gani ake musu ga talakawa. umma ta ce,bishira ina ummar taku mu gaisa?sai da ta yatsin fuska sannan ta kalli kanwarta"sumayy a kije ki cewa momy ga baki,koda yake kice mata yan gidan su Abba ne." Hajiya zainu tana zaune da kawayenta da suka zo barka, tana labarta musu rashin mutuncin dangin mijin bishira dashi kanshi mijin. ta ce,"yau kwananta uku tunda tazo gidan nan bashi ba danginshi,kuma yanda bishiran take fada mana laifin masu rikonshi wato wan ubansa da matarsa. sun mallake yaron sai abinda suka ce,hajiya nafi ta ce,"ku nuna musu kuskurensu ne yanzu haka tunda kika ga sun mallake shi kila shine mai dan samun gunshi suke ci." Hajiya sabuwa ta ce"shi yasa auran talaka ko tsiya,yar wajena Amina da tazo min da wani wai sun hadu a ummara,koda na bincika sai na tarar likita ne.karamin likita ubanshi dashi ya dogara na ce ba dani ba." Hajiya zainu ta ce"ai gara shi wannan fa tela ne." "TELA?" kawayen suka hada baki, ta ce"au dama ku duk fadan da nayi lokacin biki baku ji ba? tabi ta nace sai shi gashi nan yanzun ya wulakanta mu." Ta dube su d wulanqacin da ya fi Ki haihu kwana 3 tun dg asibiti miji bai kuma bi ta kanki ba? Hjy Nafi ta ce in bai zo don kowa ba ma yazo dn dansa. Zainu ta ce Ina nan ina jira ko shi ko danginshi domin........ Sumayya ce ta katse su da sallama. Sannan tace momy wai kizo ga yan gidan su Abba sun zo. su duka suka mike ita d kawaynta suka nufi gurin su Umma. Hjy Zainu ta kalli gurin d su umma suke,sannan ta kalli Bishira, wadannan sune 'yan gdn Su Abban? Bishira ta ce Eh ummar tasa ce gata nan. ta nuna umma Hjy zainu suka kalli juna d kawayenta sannan suka yi 'yar dry wanda hkn ya kashe jikin umman. Tasan cewa akwai wani tanadi d a ka yi mata. Hjy Zainu ta ce d kawayenta ku mu zauna,aikin zaune yafi na tsaye. Suka zauna. Ta kalli umma Dama ko ina son ganinki,ke ce uwar goyon tasa ko? ta ci gaba To gsky ba ki yi wa dnki tarbiyya

ba,sbd rashin mutunci a yi maka haihuwa amma kwana 3 ba zuwa ba aike? Kuma sai yau za ku kwaso kafa kuzo in 'yarki ce zaki so hk?umma tayi shirun tana tunani, ta kuma rasa me zata ce dn tund take ba a ta6a ci mata mutunci ba irin wannan ba. Amma ita bata iya fada ba,dn hk sai ta ce, To Hjy a yi hkr, bn san cewa Abba bai zo ba,Amma zan tsawata mishi,dn kuwa bai kyauta ba. Sai dai km shi ma bai so yadda a ka dauko masa mata ba izininshi ba,dn ya same ni d fushinsa ya ce min shi ba ya son wankan gidan nan,sannan ba a yi shawara da shi ba a ka taho d ita nan. kin ga km hkn bai dace ba..........
"Dakata min Hjy zainu ta katse ta Shi ne ya haifar min 'yar d hr zan tsaya neman izininsa? shi kuma a wa? Ramatu mokociyarsu ta ce "Miji km hjy ai ba abn wasa ba ne. hjy nafi ta ce ko?to ke kinji hjy Zainu tabdi!Tun farko kuskuran naki ne da ki ka bar 'yarki tayi irin wannan auran na rainin d tsiya. Umma ta ce d abokan tafiyarta wadanda ko dan (ba) ba su ce ba, ta ce kuzo muje"Ta dubi hjyr "Allah ya baku hkr.Hjy zainu ta ce Ai ban ga gama maganata ba. umma ta ce,To fadi ina jinki. Hjy zainu ta ce Sako ne zuwa ga danki ki fada masa ba komai muke nema dg gare shi ba,abn d ya siya ma na yaron dk mun canza wasu sdb dk 'yan gida ne. Bukatarmu ya zo ya yi wa yaronsa huduba,in km ya kai gobe za mu yi masa d kanmu. umma ta ce Abba ya yi wa dansa huduba,tn Ikcn d a ka haife shi. Hjy Zainu ta ce,To ai bai yi shawara d uwar yaron ba,ko d ya ke ga ki dawa zaiyi shawara? Uwar d ta haife shi ma bata zama komai ba, a dai ji tsoron Allah. umma jiki ba karfi ta fito. Su Ramatu suka biyo ta hr kuka sai d umma tayi dn takaici. koda taje gida sam bata fada ma kowa komai ba,illa dai dk wanda ke gidn yasan yau umma tana cikin 6acin rai. Hatta ummi da bata d kn gado sai d tayi ta tambayrta,umma baki d lfy ne?ta ce Eh,kaine ke ciwo. Da ta zauna sai ta shiga tunani so take lallai sai ta gane aibnta,ko kasawarta akn Abba. Ta kasa fahimtar mallakr d a ke fadin tayi wa Abba. Tana ganin nuna tsanarta ga Abba shi ne

mafitarta. Abba ne ya katse mata tunani d cewa Ummana ina t zuwa ba kya nan. Ta dube shi g mmknta ba ta iya bayya tsanarta g Abban, maimakon hk ma sai ta samu kanta da cewa Naje ganin jariri ne. Ya shiga ya zauna kusa d ita t dube shi Yanzu Abba dm bn isa in fada maka mgn ka ji ba?Dama kin zuwa kayi ka duba matarka da danka? Ya shafa kai,Umma anjima d dare zamu da su Ahmad ni haushi sukai bani. Ta ce to ka tabbata yau din kaje,Sannan ko sun nuna ma fushinsu naka kawai ka ba su hkr,Ya ce to umma ta ce Na sanka d zcy ne. Ya ce to zan kiyaye Umma. Ya kuma dabn ta ummata yau na ganki a yanayi mara dadin gani. ta dube shi kaina ke ciwo Abba na kuma sha magani. Da gaske ciwo kanta ya dinga yi dn damuwa. Yace Allah y kara sauki. Ya fita. Da Ahmad d Muktar suka je,sun ci sa'a Alhjn yana gari. suka shiga suka gaishe shi suka kuma yi wa juna barka. Sam ba ruwanshi da matsala,Suka shiga ciki tare d Sumyya,sn samu Aisha ta zo ita d mijinta. Bishira km hade rai tayi Ikcn d taga su Abba? Su Muktar suka dauki jariri,sannan suka gaida mai jego. ta amsa tana musu wani kallon daga ina? Aisha ce taje ta sanar d uwar tasu. Nan ko ta shigo ta samu su Abba d abokanshi. Ta shiga zazzaga mishi masi fa,wai sai yau yaga damar zuwa?Ai ta samu Ibrn yadda yake wulaqanta mata yarinya. ta ce km a bakin mahaifiyarka naji kaji tsoron Allah ka talike a gurin uwar goyonka sai yadda ta ce. to 'yata tafi karfinta. Abba sam ba zai juri ji ba,dn hk ya mike ya fita. tana ta cewa saurare ni ko waiwayowa bai yi ba. Su Muktar dai suna ciki suna bata hkr ya kira wayar Ahamad ya ce zan tafi in ba za ku fito ba. Ya kashe ba tare d jiran asmar Ahmad din ba, hk suka fito. Muktar ya ce Tabdi! lallai matar gidannan bata d mutunci.Ahamd ya ce ka fada ma mai gidan Mana. Abba ya ce Ni sai ma in sakar Musu 'yarsu "Kul in ji Muktar, Kada kayi hk Ahmad ya ce, Ashe hr umma suka yi wa rashin mutunci dazu? Abba ya ce Ummata?Muktar ya ce Eh, bayn fitarka take fada,Abba ya yi shiru dn

takaici. Gidanshi ya wuce,gado ya hau ya kwanta. . Tabbas sun ci zarafin ummarshi,dn ya ganta cikin yanayin da bai ta6a ganinta aciki ba. Ko me dame suka fada mata?Umma bata cancanci cin zarafi ba.Ranshi ya kai makura gurin 6aci,ya rufe gidn ya nufi gdn su Umma. Lkcn d ya shiga umma ta nufi dakin Alhj,Sallamarshi ce ta tsaida ita,ya shiga dakinta ta dawo ta shiga. Tana cewa Abba hr ka dawo daga gurin ma su jegon?bai amsa ba,kanshi na kasa,dmn sai ya samu kansa da jin kunyarta sakamakon abn d aka mata sbd shi. Ta ce Ify Abbana?Ya dube ta,maimakon amsa sai ya ce umma me suka ce miki dazun d ki ka je gidn? Tayi dn yaki ita a dole Murmushi , Na me Abba? ya ce mamn bishira ta ce taci miki mutunci ko? Umma tayi 'yar dry,sannan ta ce ko daya ta dai fada maka hk ne dn kaji haushi. Ta ciga ba d cewa,Abba dn Allah ka bi sannu hr t dawo...... Ya ce umma na san sunci miki zarafi sosai "ZURFIN CIKI' ne da ke umma shi yasa ki ka shanye, amma yanayinki dazn y nuna.Umma b zan zauna d matar d baya san darajarki, dk kuwa yadda na kai sonta,ina ga zamanmu ba zai yiwa d bishira ba. Umma ta ce "Kai! Kai!! kul na sake ji zanyi fushi d kai me tsanani Abba,dk hakkinsu d ke kanka matarka d danka ta ka sauke su,kuma koyaushe kaje ka gansu, ba km na son su Alhj suji wannan zancan. Ya ce yanzun hk zan zauna umma cikin 6acin rai? Tunda na auri matar nan bn huta ba,kema baki daina shan zagi ba? umma ta matso kusa da shi ta dafa kafadarshi. Abbana ka sani cewa ba a toru ka dny dn k huta ba,nawa ganin duk wanda a ka haifa daga ran d ya diro dny y gama hutu komai jin dadinsa,komai kudinsa,ko mulki. Hutu daya ne in ka mutu ka sadu d rahamar Allah,ita kuwa Rahama bata samuwa g wanda bai bi Allah d manzo ba. Bn Allah kuwa shine kada ka bata masa,kabi dukkan abn d Manzonsa ya yi umurni,Sannan ka hanu daga abn d ya yi hani. Aure bautar Allah ne Kum sai kayi hkr sannan za ka yi bauta d kyau. hk dai umma tayi ta wa Abba nasiha hr zcyrsa t sauka,

sannan sukayi Sallama. Washe gari misalin karfe 2,Abba ya dawo gida dg mkrnt d yake koyarwa, dn suna ta shirye-shiryn jarabawa (J.S.C.E.) Su ummi ne za su zana,wnk y fito sai ga wayr Alhj ta shigo.Y daga cikin girmamawa. Bayn sun gaisa Alhj ya ce Abbana kana ina ne? Ya ce ina nan gida.Alhj ya ce kaje gidanmu ka amshi mukallin dakina ka shiga kasa mukallika bude dirowar nan tawa,zaka g wadansu ta kardu irin littafin nan na rubutu. kabi a hnkl za ka g wani a samnshi an rubuta Alhj Sale Jigawa,d ajami ne rubutun,maza ka kawo min. Abba ya ce to.,Yana cikin duba littattafan sai ya ga wani an rubuta wasiyya,dk littattafan d ajami Alhj yake rubutu, Abba ya dauki littafi ya bude shafin farko an rubuta........ Babi Na Daya "Ni Alhj Sulaiman, nayi kudirin ko bayan raina 'yata Habiba (ummi) zan aurar d ita ga dan Idrisu(Abba). Da sauri Abba ya rufe littafin gabnshi yana wata muguwar faduwa,ya sake budewa ya kalli kwanan wata. Alhj yayi rubutun ne ranar d a ka haifi ummi,Ya yi sauri ya maida komai ya dauki wnd aka aiko shu yana zufa ya kalle dakin ya maida wa umma makullin ya fita da sauri Ya buga mashin can ya hango ummi suna dambe da wani yaro an raba su ta tirje kafafunta ba ko takalmi, mayafinta taci damara da shi. Ya ce "Ke! tn dg nesa ta jiyo muryar Abba,ya yi mata dakuwa ta kwashi takalmanta a hannu ta yanka d gudu. Yabi ta da kallo hr ta shige gida ya lumshe ido tare d fadin "Innalillahi wa'inna ilaihin raji'un."Me ma ya kai shi bude littafin wasiyyar Alhj Babba, Duk garin kano akwai mutumin d ya tsana irin Ummi?? To fa! ku biyomu a littafi na biyu